[8/7, 9:47 AM] Xayyeesherthul-humaerath🥀: *AUREN WATA BAKWAI*

*NOBLE WRITERS ASSOCIATION*

*© Xayyeesherthul-humaerath*

*Dedicated To NimcyLuv*

_*Auren Wata Bakwai!* daga jin sunan kun san cewa za ayi cakwakiya Iya cakwakiya,ba zan dai baku satan amsa ba, kar ku bari a baku labari, wacce ta karanta ta huta.😻_

Page-1&2

*MASARAUTAR BENONI*

Ihu take da magiya hannunta rike da get din shiga masarautar tana jijjigawa ,"Useni açҫe am mi nasta,Hokkam dama je Karshe useni,Don Allah ku barni in shiga Inga Yareema,ku bani dama ta karshe,Miyida misandiri denyo 'am,Ballite yonki am, Baffana zai mutu, ku taimakawa rayuwata." kuka take na fita a hayyaci.

Tana fada cikin muryar fulatanci wacce daga ji zaka Tabbatar da cewa hausar bata isheta ba.

Daya daga cikin dogaran ya ce, "Karya kike, Mayya anaci,turo ki akayi ki cutar mana da yareema."
Yana fada suna janyeta daga jikin get din tana kara kankamewa.
Ta ce, "Aradun Allah,na Rantse ba abun da zan wa Yareema, taimakonsa nake nema, Don Allah ku barni."

Bulala suka shauɗa mata wacce ta kara hargitsa mata tunaninta wani irin tsalle tayi ta dire da gudu tana neman hanyar gudu.

Wata farar mota ce kirar MERCEDES-BENZ ML350 ta tawo a hankali.
Adnan dake gefen glass yana hangota cikin sauri ya ce wa Driver ya dakata.

Ya na tsayawa Adnan ya fita yana, "Kee! Kee."

Idonta a rufe ta daura hannu akai.
Jikinta na rawa.

Yarinyace da bata zarce shekara Goma sha hudu ba, sanye da kayan fulani, duk ya fita a hayyacinsa kamar yadda ita ma ta fice a hayyacinta,kallo ɗaya za ka yi mata ka tabbatar da

cewa tana cikin wani mawuyacin yanayi,ko dankwali babu akanta, gashi duk a cucure ga yawo da santsi, Dogowa ce siririya mai dirin Fulani,ba a sata sahun farare can can ba kuma baza asata sahun bakake ba,duk da yanayi na tashin hankalin da take ciki hakan bai hana bayyanar da kyawunta ba.

Karasawa ya yi gabanta ganin kamar bata san yanayi ba ya cire hannunta da ta rufe fuska da shi.

Cike da mamaki ya ce, "You ,?

Cikin isa da kasaita gami da Izza ta jinin sarautar da ke yawo ajinin jikinsa duk wata ilhama da kamala ta bayyana a tare da shi, Prince Adeel Muhammad Rohaan ya fito a motar ya yin da aka bude masa.
Cikin second guda ga gukkan kwayar Idon da ya kallesa zai fahimci tsantsar jinin sarauta ne anan wanda Ubangiji ya tsara masa hallita mai cike da kwarjini da Izza, Fatar jikinsa bakine ba irin sosai dinnan ba,baƙi mai kyau da sheƙi,ga idanunsa da suka kasance Sexy Eyes da ke birkita yan mata, yana da fadin kirji da duk wani abu da 'Ya mace ke bukatar kasancewa ga Namiji ko ince fiye da haka ma.

Kananun kayane a jikinsa kamar yadda ra'ayinsa da tsarinsa yake baya taba sa kayan sarauta har sai in da wani dalili wanda ya zam dole.
Saukarsa kenan daga America wanda ba kowa ke sanin shigarsa da fitarsa ba domin tsaro.

Driver bai ajiyesa a ko ina ba sai daidai kofar part dinsa dake ta bayan masarautar kebantacce wanda ba kowa yasan da nan din ba.
Yana Parking ya fito ya Bude masa kofa  cikin hanzari.

Tafiya yake tamkar ba zai taka kasa ba.

Shigewa Adeel ya yi kaitsaye ba tare da ko kalli inda Adnan yake  ba,bare har ya yi tunanin yi masa magana ko jiransa.

Adnan ya gyara tsayuwar sa ya na kare mata kallo ya  ce, "What is your Name?"

Zaro masa manyan idanunta da taci kuka ta koshi ta yi.

Ya ce, "Oh Sorry Ya Sunan ki?"

Cikin Muryar fulancinta da gurbatacciyar hausarta ta ce, "Zainab a rugar Jauro ana she mun Gaaji."

Adnan ya ce, "Alright biyo ni mu je." Ya karasa maganar yana mata nuni da hannu.
Bayansa ta bi tana kalle kalle har suka shiga cikin bangaren Adeel.

Kai tsaye bangaren Prince Adeel suka nufa cike da mamaki take kallon wajen tamkar wata duniyar a zuciyarta take rayawa, "Oh ba don na san ban mutu ba na nace nan shine Aljannata yadda Baffa yake fadamun anya ma aljannar takai nan ko?"

ADEEL na zaune a parlour ya dan kishingida zama irin na sarauta.
ganin Adnan da Gaaji kawai sai ya tsaya yana kallon su ba tare da ya ce komai ba cike da mamaki.

Adnan ya kalli Gaaji laɓe a bakin kofa duk alamar tsoro ya gama tattara game da ita.
Ya ce, "ke ya kika tsaya abakin kofa bakya tunanin za a dake ki ne?"

Fashewa ta yi da kuka.
Ta ce, "Don Allah ni taimaka mun Baffana zai mutu."

Adnan ya juyo yana kallon Prince Adeel ya ce, "Exactly da Mamaki,meyake faruwa ne? ni dai san zuciyarka irin haka ba."

Prince ADEEL ya bi sa da ido kawai ba tare da ya ce komai aransa yana so ya yi magana,amman saboda isa da Izza irin ta jinin sarautar da ke yawo a jinin jikinsa ya kasa furta komai illa yanayinsa da ya canja na bayyanar da ɓacin rai.

Adnan kuwa sanin halin abokin nasa sarai yasa bai damu da shirun nasa ba ya ci gaba da magana.

"Atlest koda zaka daina taimakon al'umma, wannan ya zama taimako na karshe da zaka yi, sai ka ga Ubangiji ya kara buda maka hanyar samunka,idan ka taimaki wannan fulani girl din,ba ka san wani hali take ciki ba,da condition din da mahaifin nata ya shiga ba,tunda ka ga har ta nace zuwa wajen biyar, tana zuwa neman taimako baka saurarenta kana wulakanta ta,Don Allah ka taimaka ba don halinta ba, kuma ba don ta isa ba,sai Don Allah,da kuma darajarata na abokinka da nake rokonka."

A fusace Adeel ya juyo yana, "Kai Mahaukaci ne,ko mahaifiyata bata taba shigo mun parlour ba,amman kai ka dauko wata kazamiyar fulanin yarinya ta shigo mun parlour."

Yana gama fadan hakan ya yi shiru.

Adnan ya ce, "Ai awajen Ubangiji da kai da ita duk dayane babu bambanci, kawai dai anan kai mai kudi ita talaka,kai mai mulki ita baiwarka,so shine bambancin kuma ya zame maka dole ka taimaketa."

Rai bace Adeel ya furta abun da bai taba furtawa ga duk wanda ya nemi taimako gunsa, "BA ZAN TAIMAKA BA, may be ma uban nata mutuwa zaiyi,ka fitar mun da wannan kazamiyar yarinyar daga part."

Nan Shi ma Adnan rai ya baci cikin fushi ya ce, "ba zan fitar da ita ba,in kanaso ka tashi ka fitar da ita da kanka ta karfi in zaka iya ko kuma ni ka dakeni ka sa in fidda ta."

Girgiza kai Prince Adeel ya yi ya sunkuya yana wuce tare da kokarin danne fushinsa a zahiri.

Sai da suka haura sama sosai, ita kuwa Gaaji mamaki take tana kallonsa cikin ranta take sakawa daman akwai mutumin da zai iya yiwa dan uwansa mutum fatan mutuwa? Kenan zuwa zaiyi har rugar su ya kashesa? Ban da haka don kawai baffanta na kwance bai da lafiya sai yana yi masa fatan mutuwa? Wani abu take ji na yawo a cikin ranta na rashin son ganin Prince Adeel bata san miye tsana ba Amman ji take ta washe sa kamar yadda ta washi mutuwarta.

Shiru suka yi dukan su na yan mintuna

Sai da ya ja numfashi kafin ya ce  zan iya taimakonta in ta yarda Amman da sharadi zan.....
Ya yi shiru nan zufa ta fara keto masa tamkar mai nakuda.
Ya yi shiru.

Adnan ya ce, "Kai muke sauraro fa kuma yi shiru."

Goge zufar da ke kokarin jika masa jiki ya yi ya ce, "Zan... Zan....zan Aureta na tsawon Wata Bakwai kawai in ta yarda, Ana daura auren zan biya ko million nawa ne a fidda mahaifinta waje a masa magani,sannan duk inda wata bakwai ya yi zanyi signing a takadda in saketa."

Cike da mamaki Adnan ya ce, "Aure? Kuma wannan? Prince,Why?"

Da hannu ya masa alamar dakatarwa kawai ba tare da ya ce komai ba.

Gaaji ta kallesa ta yi tsalle ta diri tana, "ni? Aure ka? Inma kai mai yankan kai ne ki yanka ni? Cab Allah Saa'anam mi yiɗa ma. Allah ma ya sutura ni bana shonka."

Murmushi Adeel ya yi yana mamaki wai wannan yarinyar ce ke cewa bata sonsa, shi da yan mata ke bi amman wannan kwailar kazamiyar ce ke cewa bata sonsa.

Tashi ya yi ya shige ciki yana, "In ta yi tunani to,in kuma so take Mahaifin nata ya mutu fine wannan ba damuwata ce ba,ban da hadi da shi."

Adnan zai mata magana kenan ko tsayawa batai ba ta fice a zuciyarta tana sakawa,me ma zata yi da wannan wanda yake yiwa Baffanta fatan mutuwa.

da take ji hanjin cikinta ban da kadawa ba abun da suke.
Waige-waige take ko zata samu abun taɓawa ban da ruwan wani kogi ba abun da ta samu.
Haka ta tsaya bakin kogin tasa hannunta ta dibo ta sha sannan ta ci gaba da tafiya.

Tsakanin Rugar Jauro da cikin gari sai anyi tafiya ta kusan minti arba'in ko fi ma wani zubin akanyi awa guda indai tafiyar kafa ne,domin mota bata shiga Rugar har sai ranar kasuwa kadai sau daya a sati.

Tun tana tafiya da kwarinta har sai da ta koma jan kafa a haka ta isa rugarsu.

Shigewa bukkar su tayi jiki a mace.
Numfashin da taji na tashi sauri sauri a cikin bukkar yasata saurin karasawa ciki.
Aiko baffanta ne ranga-ranga jiki ya kara tsanani tuni ta birkice ta ma rasa abun yi tamkar za a zare ransa.

Ta kasa yi masa komai ban hawaye da ke ambaliya daga idanunta.

Ficewa tayi da wani mugun gudu.
Tuni har ta manta gajiyar da ta kwaso a hanya.

Gudu take ba kakkautawa ta fadi ta kurje ,ta kara tashi bata fasa ba,har saida ta isa cikin gari tsabar sauri a minti talatin ta isa.

tana zuwa kuwa
Bangaren Prince Adeel ta nufa kai tsaye da mugun gudu kasancewar babu kowa agun.

Tana shiga ta na numfarfashi daga kan da zata yi ta ga abun da kara firgitata tuni jikinta ya dau kyarma.

Price Adeel ne kwance da wata matashiyar budurwa suna Wasanni, babu komai jikin budurwar shi kuwa daga shi sai gajeran wando.

Jikinta ne ya fara karkarwa ta kasa motsawa tsabar tsorata bata san lokacin da ta sake fitsari ba.
Sautin Numfashinta na kara fita da sauri-sauri
Dogowan da zaiyi suka hada ido da ita nan fa ta kara firgita ta ja kafa zata gudu.
Wata irin tsawa ya mata yana janyota, "Mene ne ke kuma?" Ita ma budurwar sai a lokacin ta juyo tana kallonta."

Cikin yanayin firgici ta ce, "Naaa,naaa,naaa ga fada kuna yi ne na zo na fada ma na amince ne,na yarda."

Like, Comments And Share Please😻🙏
08103080717
Xayyeesherthul-humaerath
[8/7, 9:47 AM] Xayyeesherthul-humaerath🥀: *AUREN WATA BAKWAI*

*NOBLE WRITERS ASSOCIATION*

*© Xayyeesherthul-humaerath*

Page-3&4

Tashi ya yi daga Kan Safina Yana kokarin janyo rigarsa ya sa.

Ita kuwa wani irin takaicine ya turniketa da jin tsana cike da haushin wannan gazamiyar yarinyar da ta katse mata jin dadi, domin har cikin ranta ta gama kudurta cewa lallai yau sai tayi nasarar kasancewa da Prince Adeel amman sai dai kash wannan yarinyar ta hana hakarta kaiwa ga ruwa.
Cikin kasalalliyae muryarta ta ce, "Prince ina zaka kuma? Me wannan yarinyar take anan kasan fa bamu gama ba kuma?"

Ko kallon inda take baiyi ba take ya shige toilet, ganin hakan tasan sarai ba zata taba samun kansa ba yasa ta tashi ta maida kayanta jikinta tana bin Gaaji da wani irin mummunan kallo.
Ita kuwa kanta a kasa bata ma san tanayi ba domin har yanzu jikinta rawa yake,karo na farko da ta fara ganin mace da namiji cikin yanayi irin haka.

Yana fitowa ya sanya riga sannan ya dauki Wayarsa ya kira Shamaki ya sanar da shi ya je bangaren Uwar Soro.
Sanan ya kira Adnan ma a waya ya fada masa.

Tashi ya yi sai da yaje har kofa zai fita kafin ya juyo ya ga tana tsaye ya mata alama da hannu kan ta biyosa, sannan ta bi bayansa.

Ɓangaren Uwar Soro dake daf da bangarensa suka nufa wanda yake shima keɓantacce ne ban da Yarima ba mai zuwa in ba da wani babban dalili ba, kasancewarta wacce ta raine shi tun yana karami har kuma ya girma a yanzu babu mai sanin sirrinsa fiye da ita.

Yana shiga ciki Gaaji ta bi bayansa da mamaki Uwar Soro take binsu da kallo daga shi har gajin cikin sauri ta gyara zama tare da amsa masa sallamar da ya yi.
Yana zama sai ga Shamaki da Adnan sun shigo.

Bayan sun zo duka ban da kallonsu babu abun da Prince Adeel Ke yi.
Har cikin ransa yana jin nauyin furta masu abun da ke zuciyarsa ta wani fannin yana jin cewa hakan ba karamin kaskanci bane garesa,amman ya zaiyi? A tunanin sa hakan dai shine kawai mafitar da zai dakile duk wata kofa da ke kokarin bude masa.
Zufa ce ta ci gaba da keto masa tamkar ba yanzu ya fito daga wanka ba.

Adnan ya ce, "Prince, ka kiramu kuma ka yi shiru Go On Please."

A gajarce ya ce, "Daura mun Aure da wannan Yarinyar za ayi."

Cikin yanayi na Mamaki Uwar Soro ta ce, "Ran Yareema ya dade, Aure kuma wannan? Ina tunanin in ma itan kake so akwai bukatar a gyarata kuma a Yantata daga baiwa tukunna kafin a gabatar da ita ga MAI MARTABA da FULANI."

Dakin ya dauki shiru na kusan Second Arba'in kafin Prince Adeel ya kara da, "A haka za ayi, ba tare da sanin kowa cikinsu ba, kuma a yanzu nake so a gabatar da komai."

Dukkannin su suka koma kallon kallo.
A ƙarshe Adnan ne ya katse shirun da fadin, "Shikenan Shamaki ki kira liman yazo."

"An gama ranka ya dade."
Shamaki ya amsa da haka ya fita domin kiran liman kamar yadda aka umarta.

Ba jimawa sai gashi da liman, Adnan ne da kansa ya sanarwa da Liman dalilin kiransa domin ya san in Prince ne zai kara magana sa gaji da zaman jira.

Ba tare da bata lokaci ba Liman ya aiwatar da abun da aka umarce shi da yi, Adnan ya zam Waliyin Amarya, Shamaki ya zama Waliyin Ango Bisa sadaki Million Uku wanda Adnan ke hasashen ya wadatar a fidda mahaifin Gaaji kasar waje har a kammala masa komai na bukata.

An daura auren amman har yanzu mamaki ya gagara barin zuciyar Adnan domin ya gagara sanin dalilin da zai sa Prince ya ce zai auri yarinyar nan wanda ya tabbatar da cewa koda kyauta aka basa bazai taɓa karɓa ba, mutum da a kullum ma bijirewa batun aure yake,tare da nuna cewa bai da lokacin tsayawa kula wata mata da niyar aure,dole akwai Dalili,to Amman miye dalilin?.

Ana kammala daurin Adnan ya ce da Uwar soro , "Baba zamu tafi yanzu, ki ajiyeta agunki ana yi mata dukkanin abun da ya dace kawai."

Sun tashi zasu fita itama ta tashi tana kokarin binsu.

Rike mata hannu Uwar Soro ta yi da alamar su tafi Gaaji ta ce, "Aa Baffa, Baffana Yana shen."

Adnan ya juyo yana, "ki zauna anan kinji zamu je akai Baffanki gun mai magani ne yanzu In Sha Allah."
Haka ta bita ba don ta so ba zuciyarta fal tsoro kar suje su kashe mata baffa tunda daman Yareema ya fara yi masa fatan mutuwa, ita kuma su cinyeta.

A cikin Part din ta shigar da ita wani dake, dake babban wajene tamkar gida guda wanda ciki da wajensa ya tsaru cikin ƙawa tamkar wata duniya ta daban.

Ko da suka shiga dakin kara binsa da kallo kawai Gaaji keyi tana mamakin kasancewarta a gun shin da gaske nan kuwa duniya ? Cai wannan duniyar inaga dai wacce ake zuwa lokacin da mutum zai bar duniya ne.
Abun da take ta radawa aranta kenan.
Uwar Soro ce ta katse mata tunani tare da fadin, "Ranki ya dade mu shiga banɗaki na haɗa miki ruwa zan miki wanka."

Binta da wani mugun kallo tayi tana zare ido, wanka kuma? Ita ai ta jima da manta cewa ana wani abu wai shi wanka,ko da baffanta ke lafiya ma ita sai ranar sallah kadai suke wanka a rafi da sauran matan karkararsu, wannan shekarar kuwa da yazo bai da lafiya ko yi bata yi ba,bare kuma yanzu da ba sallah ba mai zai kaita yin wanka? Katse tunanin tayi da furtawa a zahiri, "Cab Wanka? Aradun Allah banyi haka kawai ba sallah she tazo ba zaki ce nai wanka? She kace fara?"

Uwar Soro ta ce "Ranki Ya Dade ai ba sai agwagi ne masu wanka ba, hakan tsaftane da tsaftace jiki,kuma kin ga Yareema Baya son kazanta ba za kuna shiri ba in bakya wanka zai ce ma baya sonki."

Gaaji ta cuno baki ta ce, "Ni bana shon shi daman ai tunda yake yiwa Baffana fatan mutuwa kuma sai dai shi ya mutu ya bar mun baffana raye."

Dakyar ta samu ta shawo kanta tare da Tabbatar mata cewa in bata yarda an mata wanka ba Yareema ba zai kai Baffanta a masa magani ba.

Suna shiga Toilet din ta fara ihu tana, " nan ai ba gun wanka ne ba ni ki barni kawai ai Dauɗa karin karfine karki ragemun karfina a dakeni in kasa ramawa."

Uwar Soro ta ce, "nan ne ban dakin wanka anan duk haka suke,kuma in kika yi wankan ma kara karfi zakiyi saboda muna da sabulu mai kyau."

Haka ta tuɓeta da kyar tana sa mata ruwan zafi a jiki ta kara sulle mata tana ihu, "Zaki karni ne Baba, na shiga ukuna ni Gaaji zata ƙona ni."

Haka sukata fama tana gudu tana binta har aka rage daudar dan ba ace ta fita duka ba,kanta

kuwa kin yarda ma tayi a taɓasa sam bare a wanke.

Suna gamawa ta dauko sabon brush tasa mata toothpaste ta ce, "Yawwa ungo wanke bakinki."

Tana karba ta suɗe toothpaste din tas ta shanye ta fara tauna brush din.
Uwar Soro ta bude baki, "Subhanallahi wanke baki ake ba sha ba fa." Karba tayi ta kara zuba mata wani sannan ta wanke mata bakin da kanta.

Ai kuwa datti kamar ruwan kasa jini ma bakin ya fara yi, tuni Gaaji ta rikice ta fara kuka tana ganin jiki ta ce, "Dok Allah karki shanye mun jinina kadan ne dani ba yawa kuma bai da zaƙi ma Don Allah."

Sai da dariya ta kusan subucewa Uwar soro ta danne tana, "shikenan yanzu ga ruwa kuskure bakin,kar ki shafa,ki kuskurewa kawai."

Nan fa tana sa ruwa abaki ta shanye tana, "ita ba zata zubar da jininta a banza ba ta mutu."

★★★CIKIN GIDA

FULANI ce kishingiɗe a parlour hannunta dauke da tuffa tana ci a hankali, gabadaya yanayin fuskarta sam babu walwala kallo ɗaya zaka mata ka tabbatar da cewa tana da damuwa cikin ranta.

Jakadiyar ta dake gefe tana lure da hakan ta ce, "Ranki Ya Dade Fulani lafiya kuwa?"

Ta ce, "Jakadiya kira mun Hajiya Maimuna."
Tashi tayi ta je ta kirata cikin sauri.

Hajiya Maimuna wacce take Aminiyar Fulani kuma mata agun Kawun Mai martaba ce ta shigo bangaren Fulani kamar yadda ta samu kira daga gun Jakadiya.

Zama tayi tana fadin, "Ranki Ya Dade na amsa kira, amman ya na tarar da fuskarki ba walwala fatan dai muji Alkairi."

Jakadiya na fita ta laɓe abakin kofa tana sauraren abun da Fulani zata ce.

Numfasawa tayi tana gyara zama, "Maganar Yareema ne, kina ganin kullum mai martaba kara girma yake,kwanaki na kara ja, lokacin murabus dinsa na ta kara tawowa, tsufa ya kamasa, amman Yareema sam yaki mai da hankali kan batun aure kuma kin san ba makawa shi za a daura, ba ma wannan ba ni kaina ina bukatar ganin wata wacce za ace sirika ce gareni ta haifa mun jikoki, yanzu haka fa ya kusa cika Shekara talatin a duniya."

Murmushi Hajiya Maimuna tayi ta ce, "indai Don Wannan ne ki daina damuwa Uwar giyata,ina tunanin kawai za a shirya yi masa auren ba zata ne kawai ba tare da saninsa ba kuma ba tare sanin kowa cikin Masarautar nan ba, Mai martaba kawai zaki sanar a shirya bikin na Tabbatar da cewa Yareema ba zai taɓa bijirewa zaɓinku ba amman kafin hakan a gwada tuntubarsa na ƙarshe ko yana da wacce take zaɓinsa,in ya tabbatar da cewa babu kawai sai mu shiga shirye-shiryen abubuwan da ya dace kuma a zaɓo matar data dace."

Gyara zama fulani tayi tana sakin Murmushi ita ma ta ce, "Maddallah da ke Hajiya Maimuna babu shakka hakan za ayi domin kuwa shine mafita kawai, amman Babbar Matsalar ma ban san ko yana gari ba, zan binciki Uwar Soro muji."

Jakadiya na jin motsin Hajiya Maimuna ta wuce da gudu ta nufi dakin Fulani Kilishi.

Amarya ga Fulani Babba wacce take ita ma mata ce ga Mai Martaba ta biyu.

Tana ganinta ta daka mata tsawa, "Ke Lafiya zaki shigo mun daki haka? Kina da hankali kuwa?"

Ta ce, "Ranki Ya Dade labari na samo miki ina so Hajiya Maimuna ta wuce ne kada ta ganni."

Tsaki ta daka mata tana fadin, "Oya ni fadamun to ."

A hankali murya irin ta munafukai ta ce, "Za ayiwa Yareema auren bazata ance ba wanda zai sani sai Mai Martaba da Fulani Babba."

Wani irin Murmushin takaice ..... Ta yi, "Aure? Wannan zance ne, hakan ba zai taɓa yiwuwa ba ma kada ki damu ni na san matakin da zan dauka,bama wannan ba , shin wa za a aura masa?"

Jakadiya ta ce, "basu kai ga fada ba,sun dai ce za a duba."

Dariya ta fara wacce azahirine kadai take dariya a zuciyar ta kuwa ban da tsantsar mugunta babu abun da ke ciki.

"In an fada yarinyar ki zo ki sanar mun, ba wanda ya isa aiwatar da komai cikin Masarautar nan ba tare da sani ba, don ban haihu ba hakan baya nufin in zam saniyar ware ahir."

Jakadiya na fita ta kara nufan bangaren Hajiya Rabi wacce take kishiya agun Hajiya Maimuna ta sanar da ita.

Tsaki Hajiya Rabi tayi tana fadin, "Lallai kuwa za a sha mamaki cikin Masarautar nan, Mussaman in ya kasance ba ɗaya daga cikin 'Ya'yana za abaiwa Yarima ba saidai kowa ya rasa ko ya mutu ko ya yi rai ba aure, ke ban ma ga ta zama ba,amman ina fatan dai baki sanarwa da kowa hakan ba?"

Girgiza kai kawai Jakadiya ta yi alamar eh.

Hajiya Rabi bata kara bi ta kanta ba tuni kawai ta dauki mayafi ta fice.

Tana fita Jakadiya ta tuntsire da wata irin dariya ta wani wasu surutan da ita kadai ta san fassaran su.

★★★kiran Uwar soro Fulani Babba tayi kan tana neman Yareema.

Uwar Soro ta sanar da shi kai tsaye ya nufi cikin Masarautar.
Yana zuwa zuwa daga kafar shi da zaiyi ya shiga ciki kafar ta kame kam.
[8/7, 9:47 AM] Xayyeesherthul-humaerath🥀: *AUREN WATA BAKWAI*

*NOBLE WRITERS ASSOCIATION*

© *Xayyeesherthul-humaerath*

Page-5&6

Duk kokarin da ya yi wajen ganin ya ja kafar kin motsawa tai sam sam.

Jakadiya na fitowa daga kitchen ta hangosa tsaye kafa a kame, rike baki tayi a zahiri tana fadin, "Subhanallahi Yareema lafiya?"

Ko kallon inta take bai ba bare ya bata amsa ya ci gaba da kokarin daga kafa amman ina tamkar ana kara danna kafar.

Bangaren Uwar Soro tayi tana kurma ihu, "Na Shiga ukuna,Yareema ya kame,kafar Yareema ta kame ya kasa takawa."

Uwar Soro na jin hakan ta fito cikin sauri tana fadin, "Subhanallahi ya aka yi hakan? Ina Yareeman."

Jakadiya ta ce, "Gashi can a kofar shiga bangaren Fulani Babba."
Aiko Yareema na tsaye ban da zufa ba abun da yake tun yana kokarin motsawa har ya hakura.
Uwar Soro na zuwa tayi kokarin jan kafar tasa amman ina sam hakan ya gagara.
Addu'a ta shiga tofa masa,cikin kankanin lokacin gabadaya matan cikin Masarautar sun cika

gun.

Fulani Kilishi ce ta fara karasowa garesa tana, "Subhanallahi Yareema meke faruwa haka?in kafar nan taki motsawa ta karshenta sai dai a yanketa."
Tana fada suka hada ido da Magajiya tare da sakin wani ƙayataccen murmushi.

Uwar Soro ta umarce su da duka kowa ya bar gurin abarta daga ita sai Yareema,ba yadda suka iya ba don sun so ba haka suka tafi, Fulani Babba kuwa daman bata fito ba.
Hajiya Maimuna ta ce, "Uwar soro ko zan iya tsayawa ni in taimaka?"

Girgiza mata kai tayi alamar aa haka ita ma ta bar wajen.
Addua ta ci gaba da tofa masa Kasancewar hakan ba sabon abu bane gareta tun yana karami lokuta zuwa lokuta kafarsa ta kan rike sai ta sha faman yi masa addu'o'i kafin ta sake.

Yau yafi na kullum domin kuwa da kyar kafar ta sake, tana sakewa tare suka shiga bangaren Fulani Babba.

Bayan sun shiga saida aka ɗauki kusan Second biyar kafin Fulani Babba ta fara magana.

"Yareema!."
Ta yi shiru kafin ta ci gaba da fadin, "ka san dai a yanzu ban da damuwa da burin da ya zarce ace yau ka yi aure."

Tana fada tsigar jikinsa ta fara tashi kansa na yi masa wani irin tsiro.

"Ban san mene ne dalilinka na rashin son aure ba kasancewar ka haka a yanzu baka da abun da ya kamaceka fiye da aure, na san cewa kana da nauyi akanka na juya dukkanin abubuwan da ke tafiya a masarautar nan, zuwan mata kila tana tallafa maka ta wani bangaren ka samu sauki ban sani ba ko akwai wacce kake so,indai akwaita zan so ace kayi gaggawar bayyanar da ita domin ayi komai kan lokacin da ya dace."

Shiru ya yi bai ce komai ba kansa na kasa.

FULANI babba ta kalli Uwar soro ta ce, "ko ya sanar da ke wata wacce yake muradin Aure?"
Uwar soro ta ce, "Aa Ranki Ya Dade."

"Hmm to ina jinka Adeel yanzu kai ba yaro bane kasan abun da ya ce da kai fiye da kowa." Cewar Fulani Babba.

Yareema ya ce, "Babu Ranki Ya Dade amun hakuri tukun zuwa gaba."

Fulani ta girgiza kai tana, "Shikenan Allah yasa mu dace."

Tare suka fice da Uwar soro sai ta tabbatar ya shiga bangarensa kafin ita ma ta koma nata. Tana shiga ta samu Gaaji na surfa uban kuka ita akaita gun Baffanta tana so ta ganshi kar a kashe mata shi.

Dakyar Uwar Soro ta lallabata har ta samu ta yi barci.
Cikin dare ta farka wai tana jin kashi.
Uwar Soro ta kaita toilet ta ce ta hau tayi.

"Wallahi na Rantse da Ubangiji na ba jan hau wannan abun a wawushe mun duwawuna ba,haka kawai in rasa mazaune ni kam ba zan hau ba, kawai mu fita anuna mun kasa inyi yadda muke yi a ruga."

Duk Yadda Uwar Soro tayi da Gaaji tayi kashi a toilet dinnan ki tayi fur daga karshe sai leda ta dauko mata,ta bata,ta tsuguna tayi, ga shegen yawa da uban wari tsabar da nannagi abinci harda na hauka.

Tana gamawa tasa hannu ta kulle abunta a ledar ta ajiye a gefe tana, "kuma Aradun Allah karki samun kashina cikin abunnan a ajiyemun da safe zan dauke abuna da kaina inje in binne."

Sai da ta koma barci kafin Uwar Soro ta samu ta je ta yi floshin din kashin.

Prince Adeel Muhammad Rohaan
Tun da ya koma kansa ke sara masa gabadaya wani gitaccen ciwon kai yake ji, zuciyarsa kuma ban da muradin kasancewa da wata ba abun da take.

Wayarsa ta fara ringing, yana dubawa ya ga number Safina, a jiyar zuciya ya yi aransa yana raya tamkar tasan yana da bukatar ta a yanzu.
Kara Wayar ya yi a kunne ya yi shiru.

A bangarenta ta ce"Prince inzo mu kwana? Na kasa barci Please."

Da "alright." Kawai ya amsa mata yana ajiye wayar.

Tuni ta tashi ta feshi jiki da turare ta sa wasu irin kananun kaya da zai iya gigita kowanni Ɗa namiju daga kallo ɗaya, Mussaman ma ita da take da diri bayyananne mai daukan hankali.

Tana zuwa ta kira wayarsa tashi ya yi ya bude mata kofar bayan ta shigo sannan ta rufe ta bi bayansa.

Zama ya yi a gefen gadon yana danna wayar dake hannunsa, tana shiga ta wular da Doguwar rigar da ta rufe jikinta da shi tana wata irin tafiya ta karasa garesa tana shafasa, harshenta tasa a wuyansa tana bi tana leshewa, da hannunta tana bin jikinsa a hankali, tuni ta gama sakar

masa da jiki, murya a sanyaye ta ce, "Please Prince, yau kada ka ƙi, ka yarda muyi abun da ya dace,ina da bukata kuma kai ma na Tabbatar da cewa zaka ji dadin hakan kaji."

Ba tare da yace kamai ba ya kara janyota yana sa harshen sa cikin bakinta yana kankameta, ganin hakan ta fara kokawar rabasa da kayan jikinsa, subulewa tayi daga jikinsa tana binsa da wani munafikin kallo mai kara kashe jiki ta ce, "Wait taya hakan zai yiwu da kaya jikinka bara in cire ma ko."

Shi ko tsayawa kallonta ya yi kawai tamkar hoto ta rabasa da kayan jikinta tana kokarin janye masa gajeran wando da ke ciki kenan ya dakatar da ita da hannu alamar aa.
Wani guntin tsaki tayi azahiri cikin zuciyarta tana fadin, "duk abun ka dai Wallahi yau sai na samu abun da nake so nayi galaba akanka."
Murmushi ta masa ta dawo jikinsa tana shafa girjinsa.

Shi kuwa sakewa ya kara yi,yana bin dukkan ilahirin jikinta yana kai mata wasu irin saƙonni, ban da kokarin ta hake masa ita kuwa ba abun da take, da ta kai hannunta zai rike.
Ya gama duk wasannin da yake da bukata janye jiki ya yi yana numfasawa ya ce, "Safina Is Ok Please ya isa haka barci nake ji."

Kukan karya ta fara yi tana yi masa magiya.
"Prince Wallahi  baka ji yadda nake ji ba, zan iya rasa rayuwata muddin baka biyamun bukata ta ba, ka tausayamun Please, ko na yaune kadai just once."

Jiki a mace idanun sa na rufewa ya ce, "Ki bari Gobe."

Yana fada ya kifa da kansa tuni barci ya yi awon gaba da shi.

Dafa kai Safina tayi tana, "wai wannan wani irin Bala'i ne kullum sai anzo gabar da zan aiwatar da aikina sai kace barci ko kuma wani abu ya faru? Baka da aiki sai romance? This wil be last time da zan bata lokaci na ba zan dawo gidannan ba sai da maganin da dole zai sanyaka aiwatar da abun da ake da bukata ko na huta."

Tashi ta yi tasa rigarta ta  fice,tana fita cikin duhu wani Mutumi ya karaso gareta yana, "Ya na ganki haka? Ina so inji labari mai daɗi kar ki fada mun akasin hakan."

Tsaki ta yi ta ce, "ni fa na gaji wallahi kullum sai ya kaini makura sai ya juya mun baya, Gobe ko jibi ina da bukatar anemo mun magani mai karfi da zai rikitashi duk yadda za ayi asa masa cikin abun da zai sha inaga wannan shine shawarar karshe da zata iya aiki in ba hakan ba akwai Matsala,har na gaji da binsa Wallahi."

"Shikenan kada ki damu zamuyi magana a waya." Mutumin ya fada yana waige-waige ya tafi.

WASHEGARI.

Tun da akayi sallar asuba ma'aikata da dogarai ke kai kawo cikin masautar kowa  na aikinsa.

MASARAUTAR BENONI babbar masarautace wacce ta amsa sunan masarauta a kasar hausa, ta tsaru iya tsaruwa daga wajenta har ciki,inda kudi da kayan masarufi na magana Tabbas na wannan masarautar in suka fara nasu ba sauki, Aljannar duniya ga wanda ya taba shiga cikinta domin babu mai tunanin fita koda kuwa cikin mafarki ne.

Mai Martaba Sarki Muhammad Rohaan ya gaji sarauta tun daga gun Kakansa, kakansa na rasuwa mahaifinsa ya hau karagar mulki shi ma bayan mahaifinsa ya rasu ya hau wanda yake a yanzu shi ke jagorantar BENONI.
Matansa Biyu Fulani Babba (A'isha) da Fulani Kilishi (Hafsat) Yaro Ɗaya garesa Prince Adeel Muhammad Rohaan wanda yake tamkar gado ga ahalinsu Basu cika haihuwa sosai ba, Kakansa shi kadai ne, kamar yadda mahaifinsa yake shi kadai,haka kuma shi ma ya Kasance shi kadai sannan ya haifi Ɗa shi kadai.

Mai Martaba sarki Muhammad Rohaan mutum ne mai karamci da sanin ya kamata cike da jin kan talakawa,sannan baya taba fadin magana biyu, Indai ya ce abu to babu shakka,ba canji a wannan batun, baya da yan uwa na kusa sai wa inda suka zam dangi garesa na nesa, yan uwan mahaifiyarsa ,yayunta da kanenta, dukkaninsu suna rayuwa cikin Fada da matan su da 'Ya'Yansu Waziri, Sarkin Fada, da Sarkin Yaƙi.
Waziri shine Mijin Hajiya Maimuna Yaranta mata yan biyu Nasmah da Basmah.
Sarki Yaƙi mijin Hajiya Rabi suna da yara uku mace Ɗaya Khalesa da kuma Ameen da Noor,da kuma sarki fada mijin Magajiya Da yarinyarsu Ɗaya Rumaisa.

Prince Adeel Muhammad Rohaan shike tafiya da shigar da fitar dukka wani kudi da ke wakana a MASARAUTAR BENONI kasancewar ya kammala digirinsa a bangaren tattalin arziki.

Khalesa da Nasmah suna masifar sun Prince Adeel sanadiyar yadda kowa ke bayyana soyayyarsa gareshi yasa basa shiru da juna ko kadan, wajen zama ma in daya na gun daya bata taba zuwa.

Hajiya Maimuna da Magijiya suna matuƙar nuna soyayya tare da kauna ga Adeel cike da gujewa dukkan abun da zai iya cutar da shi saɓanin sauran matan da ke bayyanar da kishinsu da tsantsar tsana a zahiri.

Aranar da Yareema yazo duniya aranar sai da aka nemeshi aka rasa a Masarautar  daga karshe sai Uwar Soro ce ta tsinto shi cikin kwali a na kokarin fidda shi daga fadan.

Hakan yasa tun Adeel na karami Mai Martaba ya zaɓi kebantar da shi tun yana da shekara Uku ya koma gun Uwar Soro har sai da ya fara girma ya kammala secondary zai shiga Jami'a kafin aka fara bayyanar da shi Wanda tunanin wasu ma da yawa a garin gabadaya ya mutu fitowarsa

kuwa ya girgiza tunanin kowa da ke Masarautar da garin.

Wannan kenan.

Karfe Bakwai na safe
Uwar Soro ta ga barci Gaaji fa bana karewa bane tadata tayi ta ce mata tayi sallah.
Kallonta tayi ido duk kwantsa ta ce, "Sallah? Tab ni fa ban girma ba ai sai an girma ake sallah ki barni inyi barcina ni."

Ta kara shigewa bargo.
Sai da taji tace mata ga abinci aiko zumbur ta tashi ta na kokarin kubcewa.

Uwar soro ta ce, "aa fa sai kinzo munje Kinyi wanka Kinyi brush kiyi alwala kiyi sallah kafin kici abincin nan?"

"Boroshe? wannan abun na jiya da kwashe mun jini ko? Na rantse banyi haka kawai aje ata kwashe mun jini saidai in wannan abun zaki sammun abaki inshanye shi kam da gardi aradun Allah kums wanka nayi jiya ai banyi yau sai ranar sallah ehee."

Uwar Soro ta ce, "to tashi muje kiyi dai koma miye sai kici abincin."

Fashewa da kuka Gaaji tayi tana, "Ni yunwa nakeji hanjin cikina kuka suke,na shiga ukuna na mutu na lalashe  ki bani abunshi inci kar in mutu."

Ta ƙarasa maganar tana birgima akan gadon harda rike ciki kamar mai nakuda.

Uwar soro ta ce , "Oh ni Jummai na gamu da gamona, ga shi zan baki kici amman kimun alƙawari in kinci zakiyi duk abun da nace kiyi kin yarda?"

Ta girgiza kai.
Mika mata tayi, tuni ta fisge ta fara ci kamar tsohuwar mayunwaciya.

Sai da ta cinye tas Uwar Soro ta ce, "Yawwa yanzu bara in dauko miki zani ki cire kaya muje bandakin ko."

Uwar Soro na shigewa dayan dakin ta kalli gefe da gefe taga ba kowa da gudu ta fice ta shige bangaren Prince Adeel.

Tana shiga ya fito daga wanka kenan yana zaune yana shafa mai ya zame towel din jikinsa babu komai a jikinsa.

Tana shiga tana ganinsa da ta kwallara wani ihu....

*DUK WACCE KE SO TA BIYA A MATA ADVERT A PAGES KOFA A BUDE TAKE YI MUN MAGANA KAI TSAYE TA NAN 08103080717*

Urs Xayyeesherthuo
[8/7, 9:47 AM] Xayyeesherthul-humaerath🥀:
https://chat.whatsapp.com/C1kXo17nLmb7vCXIubtu5o

*AUREN WATA BAKWAI*

*NOBLE WRITERS ASSOCIATION*

© *Xayyeesherthul-humaerath*

Page-7&8

Rufe idonta tayi tana kankame jikinta tamkar zata suma ta wata irin gigitacciyar ƙara.

Prince Adeel ya kalleta ya kauda kai,yaja towel din sa ya daura, yana kokarin sa kaya,ci gaba da ihun tayi kamar wacce aka sawa saban batir, har cikin Dodon kunnensa yake jin saukan kararta.
Cike da takaici ya karasa inda take yana daka mata tsawa.

Maimakon ta nutsu tsawar da ya mata yasa ta ci gaba da kwallara ihu tana kokarin shidewa.

Rufe mata baki ya yi da hannunsa yana mata alamar tai shiru.
Ita kuwa ido ta kafa masa suna kallon juna,aransa yana sakawa , "Anya wannan yarinyar na da hankali kuwa? Watakila ma mahaukaciya ce ga dukkan alama."

Ita ma a zuciyarta ta ce, "Cab lallai wannan ƙasurgumin Dan ishka ne,kawai ya zauna tsirara ba kaya, Aradun Allah watarana na kara ganinsa haka nan sai na yanke masa wannan jelar mai kama da beraye."

Kusan Minti Daya suna haka kafin ya saketa yana sauri ya shige toilet zuciyarsa na tashi, wanke hannunsa ya yi ,yana jin kyamarta dama bai kai hannunsa bakinta ba don gabadaya yanzu a tsarge da kansa yake.
Har zai fita , haka ya koma ya kara wani sabon wankan Amman duk da haka hankalinsa bai kwanta ba,hannunsa ji yake kamar har yanzu da yawunta a jiki.

Ita kuwa yana saketa,ta falfala aguje ta koma bangaren Uwar Soro tana haki kamar wacce ta

dibo kaya.

Da sauri ta riketa tana, "Ya Salam, Gaaji ina kika je? Ba wanda dai ya ganki ko? Ki daina fita in kina fita kamaki za ayi a kulle."

Gaaji ta ce, "Ni fa gun Yareema naje in ce masa ina Baffana ya jikinsa, shine fa kawai na gansa a tuɓe aradun Allah Yareema dan iska ne ashe, kin gansa kamar wani Dodo cab."

Uwar Soro ta ce, "Kul kada in kara jin hakan a bakinki kinji."

Cuno baki tayi tana, "To wayace ya zauna ba kaya,ai yan iska ne ke zama tsirara dai ga shi fa wani katon garde da shi abun tsoro ni Allah sa ma kar nayi mafarkinsa in kasa barci."
Ta fada tana rufe idonta.

Uwar Soro ta yi dariya kafin ta ce, "Na ji dai, daga yanzu in zaki je bangarensa kina fadamun kuma sai kin kwankwasa kofa ya baki izinin shiga kafin ki shiga."

"Ni ban kuma zuwa masa ma inje inga abun da zai makantar dani in daina gani ana cemun makauniya, Shikenan in kasa ganin Baffana." Gaaji ta fada tana dafe haɓa.

Rike mata hannu Uwar soro ta yi tana, "to na ji, yanzu kizo muje in miki wanka, kuma kin ga wannan kan naki ma dole a wankesa arage masa Dauda a gyara sai in miki kitso."

Take Gaaji ta bata rai tana hada girar sama da ƙasa ta ce, "ni fa nace miki bana shon wankan nan bana sho nikam fatar jikina zata zama roba, kuma ta dafe."

Uwar Soro ta ce, "Ba zata dafe ba fa zata yi kyau ne tafi yanzu haske kuma karfin ma zaki kara ne,ki zama yan mata Sosai."

Uwar Soro ta ce, "aiko in baki yarda anyi wankan nan ba bake ba abincin Rana irin me dadin nan."

Ko magana Gaaji ba tayi ba ta fara cire kaya tukun ta ce, "Mu je kin ji, Wallahi ba zan iya zama da yunwar ga ba,gwanda kawai ayi wankan nikam na hakura fatar ta ta kodewa karfin ma ya tafi amman dai abani abinshin in ci Don Allah."

Da kanta ta shiga toilet din,Uwar Soro ta mata wanka, ta dan wanke mata gashi aka rage masa dauda dan ba za dai ace ya fita duka ba, dan kwana biyun nan har ta fara chanja kala haskenta da ya dafe dan dauda har ya fara dawowa kyanta na asalin bayyana.

Dole wasu kayan Fulani Uwar Soro tasa aka nemowa Gaaji domin duk kayan da ta bata tasa cewa take ita bazata sa ba,ba shine kayan su ba.

Yau ya kasance ranar Juma'a  wacce ta kasance a kowacce Juma'a Yareema na zuwa su gana da Mai Martaba kafin su shiga Masallacin Fada suyi sallah tare.

Hakan ne ya wakana kuwa yana fitowa daga wanka ya shirya ,Shamaki na tsaye yana jiran fitowarsa yana fitowa suka nufi Cikin Fada tare.
Bayan Shamaki ya raka Yareema fada dukansu suka fice waje kamar yadda aka saba.

"Barka Da Safiya Ranka ya dade." Cewar Prince Adeel.

Mai Martaba ya ce, "Barka dai Yareema, ina fatan komai yana tafiya daidai ba tare da wata matsala?"

Prince Adeel ya ce, "AlhmduLillah komai na tafiya daidai kuma abisa tsarin da ka umarta."
Mai Martaba ya saki murmushi kafin ya ce, "Ma Sha Allah, wato kaidai ba zaka taba barin wannan shigar kasar wajen ba, ka riga ka gama sabawa da hakan ko ince kafi jin dadin hakan ko?"

Shiru Yareema ya yi kansa a kasa yana sakin Murmushi.

Mai Martaba ya ce, "Kodayake nima nayi na gaji na hakura watarana da kanka zaka daina sawa har ma ka manta da yadda ake sawan."

Shi dai Yareema bai ce komai ba sai Murmushi.
Shi kuwa Mai martaba kara jin so da kaunar ɗan nasa ɗaya tilo a duniya yake har cikin ransa, a zuciyarsa shi ma bai da muradin da ya zarce ace Yareema ya yi aure ya haifa masa jika ya gani tun yana raye,amman sam baya iya masa maganar hakan aransa ji yake cewa haka ba karamin takura bane,kuma babu abun da yafi so fiye da farincikin Yareema zai so ace da kansa ya ji sha'awar kasancewa mai iyali.

Sun dan taba hira daidai gwargwado kafin suka nufi masallaci suka saurari Huduba sannan suka yi sallah.

★★Nasmah na Tabbatar da cewa an idar da sallah ta nufi kitchen kai tsaye ta ce wa Magajiya, "Ina abincin Yareema?"

Magajiya ta ce, "ga shi can ina jira Uwar Soro ta turo a daukan masa ne."

"Aa ni zan kai masa yau,ya ce in kai." Ta karasa maganar tana kada kokarin daukan abincin.

Daga nesa taji tsawar Khalesa na fadin , "Dakata! Kada ki kuskura ki yi gigin daukan Abincin Yareema domin yau Ni nake da alhakin kai masa."

Nasmah ta ce, "What? Ban gane kamar ya?"

Bige hannun Nasmah, khaleesa tayi akan tiran abincin tana janyewa, "eheen abun da kunnenki suka jiyo shi nake nufi, Ai Babban Ɗa Sai babbar 'Ya kamar yadda nake Babbar 'Ya mace a Masarautar nan haka zan kasance mata ga Yareema atakaice dai Gimbiya duk da kin sani gwanda in kara jaddada miki don kuwa na lura da cewa kunen kashi gareki."

Ta karasa Maganar tana kare mata kallo sama da kasa tana wani irin juyi.

Magajiya ta ce, "Amman dai dukanin ku kun san cewa babu mai alhakin kaiwa Yareema abinci ba tare da izinin Uwar Soro ba ko?"

Khalesa ta ce, "agunki kenan don ni ai a yanzu nafi Uwar Soro kusanci ga yareema zan gansa a lokacin da na so kuma nayi niya Don haka ni zan kai abincin Yareema ba wanda ya isa ya hanani kaiwa."

Nasmah ta ce, "ai bai zam mallakin ki ba a yanzu Don haka kowacce na da hakkin amfani da damarta duk wacce tai nasara shikenan." Ta karasa magana tana kokarin fisgewa.

Wani azababben mari Khalesa ta sake mata a afuska da sauri Magajiya ta karasa inda suke daidai da lokacin da Jakadiya ta shiga kitchen din.

"Kai kai kai.. mai zan gani haka me ke faruwa ne?" Jakadiya ta fada.

Nasmah na kuka ta ce, "na zo daukan abincin Yareema ne zan kai masa Khaleesa ta kwace wai ba zan kai ba kuma ta mareni."

Khalesa ta ce, "Karya kike  karamar munafuka."

"Aa fa ba ayi haka ba kema dai Nasmah kin fiye tsaurin ido taya Khalesa zata kaiwa Yareema abinci kice ke zaki? Ai ido ba mudi ba amman yasan kima,ita da muke fata nan da kwanaki kadan muji ta zam gimbiya, aa aa Maza Khalesa je ki kai wa Yareema abinci."

Kuka Nasmah ta kara fashewa da shi ta fice da gudu a kitchen.

Khalesa tayi tsaki tana, "Kya yi kya gama Yareema dai kam nawane." Suka hada ido da Jakadiya suna sakewa juna Murmushi.

Nasmah na zuwa ta fada jikin Hajiya Maimuna tana kuka tana fada mata abun da Khalesa da da Jakadiya suka yi mata.
Hajiya Maimuna ta  share mata hawaye tana murmushi, "Hakanne ya saki kuka? Mene ne na kuka akan haka? Lallai baki tanadi zuciyar da zaki tallafi soyayyarki ba, ki zam jaruma,mai maida komai ba komai ba koda kuwa komai dinne,ki sa aranki cewa indai Yareema mijinki duk

rintsi duk wuya babu fashi sai ya kasance naki, rabon kwado ai baya taba hawa sama,ko ya hau ma dole ya fado, don haka ki kwantar da hankalinki."

★★

Fita tayi tana tafiya tana rangwada tamkar bazata taka kasa ba,tana zuwa Tayi Nocking shiga bangarensa, Shamaki ya fito ya sanar da ita yana barci ta bada abincin a ajiye masa.

Khaleesa ta ce, "ka tashesa ka ce nice ina son ganin sane Don Allah."

Shamaki ya ce, "Kin san dai in ba wani uzuri babba ba ba damar tada Yareema a lokacin da yake hutawa mussaman rana irin ta yau."

"Ni dai Don Allah yau kadai amun wannan alfarmar."

Komawa ciki shamaki ya yi,ya yi dace kuwa yana zuwa ya tarar da Yareema zaune yana danna laptop ga dukkan alamu yana duba wani abu mai mahimmanci ne.

Shamaki ya ce, "Ranka Ya dade Khaleesa ce awaje ta kawo ma abinci."

"To ka karba mana."Yareema ya fada hankalin sa na kan system din dake gabansa.

Shamaki ya kara da, "Aa ta ce wai kai take son gani abata izini ta shigo."

Da Okay kawai Yareema ya amsa, Shamaki ya fita ya cewa Khaleesa ta shiga.

Tana shiga ta ajiye Abincin kan daining sanan ta karasa daf inda yake ta zauna tana, "Good Afternoon Darling Prince."

"Afternoon." Ya amsa kawai.

Shagwabe fuska ta yi tana, "I Call You but you didn't pick Why?, i just want to hear Your Sweet Vioce, nikam ko laifi Nama ne?"

Tana ta surutun ta yana ji amman hankalin sa baya kanta kuma bai da niyar bata amsa.
Ta ci gaba da magana. , "Wai yaushe zaka gabatar masu da cewa nice zaɓinka ne? Nikam na matsu ina so ayi adaura mana aure."

Sai a lokacin ya juyo ya kalleta cike da mamaki ya ce, "Aure? Dawa?"

"Da kai mana, ka san dai nice babbar 'Ya mace kamar yadda kake namiji So mu muka fi dacewa da juna ni yanzu ma da zaka barni dawowa nan part din zanyi ya yi mun kyau gaskiya in munyi aure zanji dadin zama anan Sosai."

Ganin bai da niyar kara kulata ta fara mannewa a jikinsa tana magana cikin sanyayyar murya.

Prince Adeel ya yi saurin.......

Comments,Share&Like, Fisabillah.😻🙏

08103080717

Urs Xayyeesherthuo
[8/7, 9:47 AM] Xayyeesherthul-humaerath🥀:
https://chat.whatsapp.com/C1kXo17nLmb7vCXIubtu5o

*AUREN WATA BAKWAI*

*NOBLE WRITERS ASSOCIATION*

© *Xayyeesherthul-humaerath*

Page-9&10

Ya yi saurin kauce mata yana zame jikinsa.
Kara damƙosa tayi ta ce, "Please Just Once Prince."

"Stop it, i said stop it Nasmah, bana so ki je Ki tafi Don Allah inna gama aiki zan nemeki da kaina."
Murya a shagwabe ta ce , "Promise?"
Girgiza mata kai ya yi kawai yana gyara zamansa.

"Alright ga abincin ka nan byebye." Ta fada tana kokarin fita.

Har taje bakin kofar ta dawo, rungumesa tayi tana kissing dinsa sannan ta raɗa masa a kunne, "For me, you're like a lethal deadly drug. Once taken, you're addictive,I Love You So Much Darling Prince."

Ta karasa maganar tana kara kai masa kiss ta fita tana sakin wani irin ƙayataccen murmushi.

"Yes, komai ya kusa tafiya daidai, burina zai cika Soon To Be Mrs Adeel Muhammad Rohaan (Gimbiya)"
Ta fada fuska fal farinciki.

Ci gaba da aikinsa ya yi hankalinsa kwance.
Adnan ne ya shigo dakin yana fadin, "An kammala komai fa kan Baban Zainab har ma an fidda shi India komai da ake bukata ina tunanin an samu."

"Okay." Kawai Yareema ya amsa da shi.

Adnan ya kara fadin, "Ina take ne? Ta zo nan kuwa? Amaryar tamu." Ya karasa maganar cikin sigar tsokana.
Da harara Yareema ya bisa da shi yana, "Mahaukaciya dai." Daga nan ya yi shiru ya ci gaba da abun da ke gabansa.

Dariya Adnan ya yi, ya fice yana, "Haka dai ka gani kana so bara ma inje mu gana in gaida Gimbiya Matar Yareema."

Bangaren Uwar Soro ya nufa yana shiga kuwa ya tarar da Gaaji zaune ta baje Uwar Soro ta aje mata wasu manyan teddies ban da sambatu ba abun da take masu.
Tana ganinsa ta mike tana rike haɓa, "ka kawo mun Baffana ne? Ya ji sauki dai ko? Ina yake? Ka kaini gunsa in gansa ka ji."

Adnan ya karasa gareta yana, "Baffanki na asibiti an fara yi masa aiki zaiji sauki In Sha Allah."

"To akaini gunsa mana,nikam akaini inga Baffana." Cewar Gaaji da idanunta suka cika da hawaye tana kokarin yin kuka.

Adnan ya durkusa gabanta yana rike mata hannu, "Aa fa kar ki mun kuka, kin manta ke babbar yarinya ce yanzu? Kuma Kin manta alkawarin ku da Yareema? Sai nan da Wata bakwai kafin Baffanki ya gama jin sauki shikenan zaki koma rugarku kije ki zauna da Baffanki."

Gaaji ta Taɓe baki, "Tom ni dai ka gaishe mun da Baffana in kaje Kuma in baka labari?"

Adnan ya ce, "Eh."
Daidai da fitowar Uwar Soro daga cikin daki kenan.
Gaaji ta kalleta ta ce, "Kawo kunnenka in fada ma Kar taji Sirrine."

Dariya Adnan ya yi ya kalli Uwar Soro ya ce, "Barka da fitowa Baba."

"Barkanmu Dai Adnan kana tare da mutuniyar ne?"

Adnan ya ce, "eh Wallahi na shigo bakya kusa."

Gaaji ta katse su da fadin, " Ni kajo kaji in fada ma , in ba haka na fasa."

Murmushi Adnan ya yi ya ce, "Oh Sorry gani Ranki Ya Dade Gimbiya."

"Ni ba Soro ce ba ehee saidai kaine Soro nidai sunana Gaaji kuma ba gimbiya ba." Ta fada tana murguda baki.

Dariya ya yi ya ce, "To afwan gani nan."

Tsalle tayi ta janyo kunnensa ta fara raɗa masa, "Aradun Allah Yareema Dan ishka ne,tsirara fa yake zama a dakinsa naje na gansa kuma ranar ma na gansa yana faɗa da wata ita ma tsirara, kai dai ba dan ishka bane ba ko?"

Dariya ce ke kokarin subucewa Adnan ya ce, "Ni ai ba ruwana."
Sake masa kunne tayi tana, "Yawww to ni kai ma ina sho kai zan aura in Yareema ya sake ni."

Uwar Soro ta ce, "Kai dai yau ka gamu da gamonka."

Dariya kawai Adnan ya yi.
Gaaji ta mika masa hannu , "mu ma kulla ƙawance daga yau kaine babban abokina."

Mika mata yayi suka kulla Gaaji tana washe baki.

Ya ce, "To Shikenan dai yanzu bara in tafi ko ,ki kula da kanki."

Gaaji ta ce, "Tom sai ka dawo,ka dawo fa muyi wasa ka ji."

Murmushi Adnan ya yi,yawa Uwar Soro sallama sannan ya fice yana murmushi.

Bangaren Adeel ya koma.
Yana zuwa ya tarar da shi yana cin abinci.

Zama ya yi kan 2siter ya ce, "Safina tazo gidannan ko?"

Adeel ya amsa masa da ,"Eheen."

Nan take fuskar Adnan ta canja cikin fushi ya ce, "Na rasa mene ne yake damunka Prince na rasa mene ne damuwarka da ma abun da zaka so ji ajikin waccer yarinyar yar bariki, Mace ta dunga kawo kanta gareka kuma kana amince mata, shin wai kana mantawa da matsayinka ne? Ka manta kai wane ne?"

Ko kallonsa Adeel bai ba ya ci gaba da cin abincinsa cikin kwanciyar hankali tamkar bai san da zaman Adnan ba bare batun da yake.
Adnan ya kara fusata ya ce , "Ni dai bazan fasa fada ma gaskiya ba, Duk abun da zaka yi kana tuna kai wane ne da kuma darajar mahaifinka da Masarautar nan in ba so kake ka zubdawa kowa mutunci ba, in ma macen kake da bukata ba ga waccer yarinyar ba ka aura kayi koma

miye da ita Ba wasu yan iskan titi ba."

Cikin fushi  Prince Adeel ya dago fuska ya ce, "Ya isa! Na ce maka hakan ya isa, ni ban aureta Don ina sonta ko kasancewa da ita ba, sannan Safina da sauran ma baka da sanin abun da ke gudana a tsakaninmu."
Ya yi shiru yana ajiyar zuciya kusan Second Uku kafin ya ce, "Ka bar shiga abun da bai shafe ka ba."

"Ok ok haka zaka ce? Ba za dai ka fasa ba kenan?  Ko a addinance kasan....
Adnan ya yi shiru bai karasa ba can kuma ya ce, "koma miye kayi duk abun da kake so nawa ido ne da fatan Allah ganar da kai."

Ko kaɗan Adnan baya son abun da zai iya taɓa rayuwar Prince Adeel domin jin hakan yake aransa tamkar shine.
Hakan yasa duk fada basa taɓa iya fushi da juna.

Yana cikin cin abinci yaji wayarsa na kara alamar shigowar sako.
Dubawan da zaiyi ya saki tsaki domin Number ce wacce aka saba turo masa da saƙo a kullum da kalaman soyayya.
Kamar kullum yau ma haka aka rubuto masa, " Duk da cewa baka maida mun da amsa a duk sanda zan turo sako hakan ba zai taɓa sawa na karaya ko inji cewa ba zan iya samun cikar burina ba, Prince Adeel Muhammad Rohaan INA SONKA, INA KAUNARKA, kuma da kai zan rayu har karshen numfashina,kasa aranka cewa ni kadai ce taka,kuma na dace da kai,muddin ina numfashi cikin duniya baka da wata matar da ta zarce ni, Inko ni ban zam matarka ba to ka tabbatar da cewa ba zaka taba yin aure ba,kamar yadda nima ba zan taba yi ba muddin in ba tare da kai ba, na taso da sonka tun kafin insan mene ne so, haka kuma na girma da sonka cike da tsoro da fargaban rasaka domin nasan cewa zan ci gaba da rayuwa ne kawai muddin kaima kana numfashi a doron kasa, ni kadai ce taka,kuma ni kadai zan amsa sunan Gimbiya Matar Yareema, Ina Kaunarka."

A kasa sakon aka rubuta

Gimbiya S.

Ajiye wayar ya yi gefe yana cewa, "Adnan ina so mu dan fita kaina juyawa yake."

"Okay." Adnan ya fada yana tashi.

★★★

Jakadiya na ganin Khalesa ta koma bangaren su tabi bayanta.

Sai da ta basu labrin yadda suka yi da Yareema ita da Hajiya Rabi kafin Jakadiya ta numfasa ta ce, "Yo ke hajiya ai sakarki ta yanke saƙa domin ina tunanin hakarmu na dab da cin ruwa, yanzu wannan aikin nakine , kai tsaye ki nufi Bangaren Fulani ki sanar da ita wannan labari cikin siga mai jan hankali zaki dawo ki bani labari."

Hajiya Rabi ta bude baki tana fadin, "Kuma fa har na dau hasken dadina dake kanki na matukar kawo wuta, ba zan bari abun nan yyi sanyi ba, yanzu yanzu ina zuwa."

Hajiya Rabi ce zaune A parlourn Fulani Babba kanta na kasa take fadin, "Allah ya ja da ran Fulani Daman wata magana ce na zo da ita ban sani ba ko nayi laifi ko kuma zaki ga dacewar hakan."

Fulani ta ce, "Ah Bismillah mana ina sauraren ki In Sha Allah."

"Umm Daman nace batun Yareema da Khalesa ne, ban sani ba ko kina da masaniyar cewa sun daidaita juna, umm kuma daman kin ga a tsari ma sune manya ita ke bi masa in aka hadasu aure zumunci zaifi kara danko."

Cike da mamaki Fulani ta ce, "Khalesa da Yareema kuma? Amman ko in hakan zai kasance zanji dadi gaskiya ,kuma shine na tambayesa ko da wacce yake so ya ce mun Babu?"

Hajiya Rabi cikin in ina ta ce, "Ranki Ya Dade ai da ke kinsan Yareema da miskilanci ba zai taba furta hakan da bakinsa ba."
Fulani ta girgiza kai, "kuma hakane kam Tabbas akwai bukatar in sanar da Mai Martaba cikin gaggawa na Tabbatar da cewa sai yafi kowa jin dadin hakan ba jan lokaci za ayi duk abun da ya dace, wannan albishir ne mai kyau ai." Ta fada cikin bayyanar da Farinciki fal fuskarta.

Daga nan suka ci gaba da taba hirar yadda ya kamata abubuwa su kasance.

Jakadiya na jin motsin alamar fitowar Hajiya Rabi cikin Sauri ta nufi bangaren Fulani Kilishi.
Ta kwashe dukkanin abun da ta jiyo daga dakin Fulani Babba kan ana shirin bawa Yareema Khalesa.

Fulani Kilishi ta ce, "Ah lallai Hajiya Rabi na son shiga gonata, Tabbas tana so takai kanta da Ɗanta kogin mutuwa na Tabbatar da cewa bata san ni wace ce ba har yanzu ganin cewa ina raga masu amman yanzu kam anzo gabar da zanyi fito na fito da kowa ba tare da shakka ba."

Jakadiya ta ce, "abun takaicinma Yarinyar nan bata ji fa, bin maza take kamar karya a kalla an zubda mata ciki yafi sau uku."

Zaro ido Fulani Kilishi tayi ta ce, "kee? Ina masarautar ban sani ba? Garin yaya? Bani bayani domin hakan ma wani babban taimako zai mun."

Magana take ciki ciki kamar zata shake ta ce, "Sirri ne zan fada miki amman mu ...

Ta fara leke leke kafin ta karasa, "Mu shige can ciki."

Like, Comments And Share Fisabillah.

Guntun Comments,Guntu Typing🌝

08103080717
[8/7, 9:47 AM] Xayyeesherthul-humaerath🥀:
https://chat.whatsapp.com/C1kXo17nLmb7vCXIubtu5o

*AUREN WATA BAKWAI*

*NOBLE WRITERS ASSOCIATION*

© *Xayyeesherthul-humaerath*

Page-11&12

Suna shiga Jakadiya ta ce, "Ai ban da bin Maza ba abun da yarinyar nan tasa agaba, watarana fa bata kwana cikin Masarautar nan, In tayo ciki ni da kaina ake sawa in akesawa in kawo maganin zubdawan, Amman fa kar ki bari kowa ya sani."

Fulani Kilishi ta ce, "Umm babu mamaki, karki damu, kije ke dai ta bangarenki kimun kokari duk yadda za ayi da duk wata hanya da zata kawo tsaiko ga auren kiyi sauran aikin kuma nawa ne nasan me zan yi."

Jakadiya ta ce, "To,to,to ki fadamun shirin naki mana kinga sai muyi komai a tare har mu kai ga cin nasara."

Wata irin Dariya Fulani Kilishi ta yi ta ce, "Ni in fada miki shirina? Ai kinyi kadan wa inda ke gabanki ma sunyi kadan, Allah kadai ya san shirina kuma daga shi babu kari, kiyi aikinki ke dai kawai."

Duk Yadda Jakadiya ta so da ta ji shirin Fulani Kilishi ta kasa samun galaba haka ta fice zuciya fal takaicin Fulani Kilishi domin bala'in wayo gareta zata iya shan cikin kowa ta ji abun da ke ransa amman ita baza a taɓa jin ko tarinta ba har sai ta so hakan.
https://chat.whatsapp.com/C1kXo17nLmb7vCXIubtu5o

*AUREN WATA BAKWAI*

*NOBLE WRITERS ASSOCIATION*

© *Xayyeesherthul-humaerath*

Page-11&12

Suna shiga Jakadiya ta ce, "Ai ban da bin Maza ba abun da yarinyar nan tasa agaba, watarana fa bata kwana cikin Masarautar nan, In tayo ciki ni da kaina ake sawa in akesawa in kawo maganin zubdawan, Amman fa kar ki bari kowa ya sani."

Fulani Kilishi ta ce, "Umm babu mamaki, karki damu, kije ke dai ta bangarenki kimun kokari duk yadda za ayi da duk wata hanya da zata kawo tsaiko ga auren kiyi sauran aikin kuma nawa ne nasan me zan yi."

Jakadiya ta ce, "To,to,to ki fadamun shirin naki mana kinga sai muyi komai a tare har mu kai ga cin nasara."

Wata irin Dariya Fulani Kilishi ta yi ta ce, "Ni in fada miki shirina? Ai kinyi kadan wa inda ke gabanki ma sunyi kadan, Allah kadai ya san shirina kuma daga shi babu kari, kiyi aikinki ke dai kawai."

Duk Yadda Jakadiya ta so da ta ji shirin Fulani Kilishi ta kasa samun galaba haka ta fice zuciya fal takaicin Fulani Kilishi domin bala'in wayo gareta zata iya shan cikin kowa ta ji abun da ke ransa amman ita baza a taɓa jin ko tarinta ba har sai ta so hakan.

★★★
★★★

Sai can wajen karfe Tara na dare Adnan da Prince Adeel suka koma cikin masarauta.
Gaaji na tsaye jikin window taga shigarsu da sauri ta fita, Adnan ya fara shiga Adeel ne ke kokarin shigewa rike masa hannu ta yi cikin Shagwaba ta ce, "Aboki ba ka mun alƙawari zaka dawo muyi wasa ba?"
Dake dukkaninsu Bakaken Riguna ne a jikinsu,hakan yasa bata iya bambamcewa ko tunanin cewa Prince Adeel ne ba Adnan ba

Adeel ya juyo da sauri yana yi mata wani irin kallo nan take ta razana jikinta ya fara rawa.
Fisge hannunsa ya yi, cikin tsawa ya ce, "Tafi anan."
Adnan na ji ya tashi da sauri tana kokarin komawa da gudu kenan  ya ce, "Gaaji? Me ya faru?"

Tsayawa tayi daga nesa bayan Adeel ya shige ta ma Adnan alama da hannu, "jo ka ji."

Yana zuwa ta ce, "ni fa na zata kaine shine na rike masa hannu shi kuma yamun tsawa kuma ya bani tsoro da wannan idon nasa."

"Bai ganeki bane inaga fa, yanzu madadin sa na ce miki kiyi hakuri to,kin hakura?"

Murguda baki ta yi ta ce, "ai ni shi nake so ya bani hakuri ba kai ba wayace ya mun tsawa tom."
Ta karasa maganar tana taɓe fuska.
Murmushi Adnan ya yi ya ce, "Oh Gaaji to ba ni bane abokinki?"

Baki a cune ta ce, "Kaine mana, ai shi ba ruwana da shi."

"Yawwa To Kiyi hakuri kinji ." Adnan ya fada.

Alama da kai ta masa tana kara shagwabe fuska.
Ya ce, "Yawwa to yi mun murmushi mu ga."

"Umm umm ni sai kace zaka zo muje muyi wasa da Yarana sai inyi ma Murmushin."

Adnan ya ce, "Eh na yarda to yi murmushin."

Washe baki tayi wanda ya bayyanar da asalin kyawunta da dimple dinta da ya shiga ciki.

"Yawwa To Oya Give me five."
Adnan ya fada.
Tsira masa ido tayi bata san me ya ce ba.

Ya yi dariya , "Au to bani biyar mu tafa."
Mika masa tayi dukan su suna dariya.
Ya rike mata hannu suka koma ɓangaren Uwar Soro.

Ta ce, "ai na hango ku shiyasa ma na zauna ina jira ta dawo gwanda da ka biyota ka ga ta gama cin abinci wanka zata yi ta yi brush take gudun nan."

Adnan ya kalli Gaaji yana zaro ido, "Daman wanka kike gudu? To ni bana kawance da mara wanka da brush gaskiya,ba ruwana dake daga yau,mu kunce ma."
Ya karasa maganar yana mika mata hannu.

Tuni idanunta suka cicciko kamar zata yi kuka ta ce, "Aa zanyi, amman wannan abun Buroshe din fa kwashe mun jini yake zan mutu ne, kuma ni kar ka yi fushi dani kace baka kawa dani."

Adnan ya ce, "Dattin bakinkine yake fita ba jini ba, indai da gaske ni abokinki ne to kije kiyi ina

jiranki."
A shagwaɓe ta ce, "Tom nidai saidai kai kamun muje tare." Ta fada tana rike masa hannu.

Adnan ya ce, "Aa za dai amiki ai namiji baya yiwa mace wanka,ba kyau in ganki haka fa kije amiki ina jiranki har ki fito."

Gaaji ta ce, "Tom kar ka tafi kaji ina zuwa yanzu zanje amun."
Da kanta ta shiga toilet din, Uwar Soro ta bita tana murmushi domin tasan da ba Adnan sai dai suta dambarwa da kyar ta yarda.

Aikuwa Uwar Soro na mata wanka tana surutai tana ba Adnan labari yana amsawa adole kar ya gudu.
Har ta fito aka shiryata sannan ta koma parlour gunsa.

Adnan ya ce, "Yawwa ko ke fa Good girl."

"Mene ne? Ni ba gudu nake ba fa." Ta fada.

Dariya Adnan ya yi ya ce, "Cewa Na yi Good girl ma'ana yarinyar kirki."

Ta washe baki "to kai ma Guduo gu tunda kai ma yaron kirki ne ba irin wancen Yareeman ba."

Adnan ya yi dariya kawai yana binta da kallo ita kadai ta ce wannan ta ce wancen magana daya biyu sai ta ce Baffanta wanda hakan ya kara tabbatar masa da cewa bata da kowa fiye da baffanta.
Ta ce, "Ka ga kullum Baffana sai ya mun tatsuniya nake barci tunda ya fara ciwo kuma ya daina mun shikenan." Tana fadan hakan yanayinta ya canja damuwa ta bayyana a fuskarta.
Tsantsar tausayinta Adnan ya ji har cikin ransa ya ce, "Yanzu zanna miki tatsuniya madadin Baffa kafin ya ji sauki kin yarda?"

Da sauri ta ce, "Eh da gaske kake?"

Ya ce,"Ehen."
Gyara zama ya yi,itama ta matsa daf da shi.
Ya fara yi mata tatsuniya ban da dariya ba abun da Gaaji take yi,a haka har barci ya kwasheta ta fada jikinsa.

Dakansa ya dauketa ya kaita daki ya kwantar da ita, saida ya shafa mata addu'a kafin ya fita.
Gidansu ya nufa kawai ganin dare ya yi bai koma bangaren Prince ba.
★★
A wannan tsalelen daren.
Motar safina ce a gefe tana ciki waya take tana fadin , "inata kiransa fa bai dauki Kiran ba nikam na gaji zan tafi."

A dayan bangaren aka ce, "Kar ki damu ba sai ya dauka ba,na Tabbatar yanzu dai ya ci abincin daren da aka kai masa,inma bai ci ba to ya sha drinks din ko ruwan so kina shiga komai zai tafi daidai Don Allah karkiyi mana wasa da wannan damar domin ita ce ta karshe a garemu."

Dariya Safina ta yi,ta ce, "an gama Tabbas yau akwai shagali kace mun ka gama naka aikin saura nawa." Ta karasa maganar tana katse wayar tare da cizon bakinta.

Kai tsaye ta shige ciki tana shiga kuwa ta tarar da Prince Adeel kwance ga dukkan alamu yana cikin wani yanayi hannunsa akan gabansa yana juyi .

Tsayawa tayi daga nesa tana wani irin Murmushin Mugunta.

Adeel na jin alamar ta ya dago cikin wata irin gigitacciyar murya ya ce, "Safina Am in need Please."

Yana fada ta kara kwantawa.
Karasawa gare sa tayi cikin jin dadi.
Ta dagosa tana....

Comments,Like,And Share Fisabillah🥺🙏

08103080717
Urs Xayyeesherthuo
[8/7, 7:29 PM] Xayyeesherthul-humaerath🥀:
https://chat.whatsapp.com/C1kXo17nLmb7vCXIubtu5o

*AUREN WATA BAKWAI*

*NOBLE WRITERS ASSOCIATION*

© *Xayyeesherthul-humaerath*

Page-13&14

*AUREN WATA BAKWAI GROUP, Son So fisabillah,Masoyan Yareema da Uwani Gaaji😂💔dama masoyan Safina da Khalesa tare da Uwar Gayya Jakadiya😂😘😻🥀*

Tana bin jikinsa.
Ya ce, "Ki dan gyara mun kwanciyar, ina so inyi barci." Ya fada murya a ƙasa cikin yanayin galabaita.

Tallafa masa tayi ya kwanta, ruf da ciki, nan take wani irin barci ya yi awun gaba da shi,tamkar matacce.
Kamar wasa ta kwanta ita ma tana jira ya farka amman ina,babu alamun motsi bare tashi har dare ya fara tsalawa wajen karfe biyu da wani abu.

Jijigashi ta fara yi tana, "Prince Ka tashi mana, wannan wani irin barci ne kuma, Ka tashi Please."
Bai ma san tana yi ba hasali ma nauyinsa duk ya sake yana barcin da kyar take iya girgizasa.
Ganin bata da yadda zata yi ga dare ya yi bata so ta kwana asamu akasi wani ya ganta haka ta tashi ta fita zuciya fal takaici da bakin ciki.

Tana shiga Motarta ta ,ta nufi hanyar gida rai ɓace.
Shigar ta kenan Wayarta ta fara ringing dauka tayi a dayan bangaren aka ce, "ina fatan komai dai ya tafi daidai?"
Tsaki Safina ta yi ta ce, "wani daidai? Da farko naje kamar abun arziki naga alamun ya ci abun da zai sa sa aikata abun da muke so dole, amman kuma sai barci ya dauke sa nan take ta yadda bazan iya aikata komai da kaina bama, don nayi kokarin hakan amman yanayin kwanciyar da kuma yanayin yadda surar jikinsa take na gagara aikata komai, anya ba kuskure akayi aka sa masa maganin barci madadin namu ba?"

"Taya zaki ce maganin barci kuma? Abun da ni da hannuna na zuba kuma ni na siyo,ni na fara tunanin kema dai kawai da naki bakya son ayi abun nan kowa ma ya huta, kuma kin san cewa nawa mai sauki ne a karshe kece da reward din samun nasara indai hakan ya tabbata."

Cikin Fushi Safina ta ce, "Oh ka dawo da laifin gareni kenan? Duk kokarin da nake a banza? Alright Shikenan ka gwada wata mana in Zata iya har ma ta jure miskilancin wannan mutumin gwanda ma ni ai."

Ya ce, "Na ji yanzu meye kike ganin mafita tun an kara samun wani tsaikon?"

Safina ta ce, "Akwai bukatar a kara komawa ta inda aka hau domin tanan ne kadai za a sauka, yana da taurin kai sosai kuma babu shakka akwai wani abu tattare da shi da dole sai an kawar kafin akai ga cin nasara."

"Umm tabbas yanzu nima na fahimta kuma indai hakanne za ayi gagawan tabbatarwa duk wannan taurin kan da duk wani abu da ya ke ji da shi sai ya gagaresa ba matsala ki huta yanzu kam baza ki kara kai kanki ba har sai ya nemeki."
Yana karasa maganar ya katse wayar.

Safina kuwa gyara kwanciya ta yi abunta sai barci.

Karfe Hudun dare Prince Adeel ya farka ban da zufa babu abun da ke keto masa, ya tashi ya yi wanka sannan ya dauro alwala.
Salloli ya fara yi har sai da aka kira sallar asuba ya fita yaje masallaci ya yi.

★★★Gaaji na tashi daga barci ta ce lallai ita baza ta yi wanka ba sai Abokinta Adnan ya zo.
Uwar Soro ta rasa yadda zata yi a karshe dai sai da ta kira Adnan suka yi Waya da Ita ya ce in bata tsaya an mata kwalliya ba,bazai zo gunta ba kuma ya mata alkawarin zai fita da ita ya siyo mata kaya masu kyau abubuwan ci na dadi.

Da tsallenta ta ce, "Yanzu zan yi wankan kuma zan tsaya amun da kyau in fita ka yi sauri kazo fa."

Tunda tayi wanka ta tsaya ta window tana leken ta inda Adnan zai bullo har wajen karfe uku.
Da kyar Uwar Soro tasa ta tayi sallah da dabarar cewa in bata yi sallah bama Adnan ba zai zo ba.
Duk da cewa sallar ta ta ma fanko ce domin kifawa kawai take tana tashi, a hankali tana dan nuna mata wasu abubuwan tana gyarawa.

Sai wajen karfe Biyar Adnan ya shigo, bai ma je gun Yareema ba gunta ya wuce kai tsaye.
Tana ganinsa ta bata rai, "Ni nayi fushi,na daina Shonka kuma ma mun kunce." Ta karasa maganar tana mika masa hannu alamar su kunce.
Durkusawa gabanta Adnan ya yi ya kama kunnen ya ce, "Afwan Gaaji Beauty kin ga na kama kunne na ko sai na mari fuskata?"

A shagwaɓe ta ce, "E amman kar ka mara da zafi a hankali kuma sai kace zaka goyani yadda baffana ke mun,kuma zaka na zuwa guna da wuri."

Marin fuskarsa ya yi yana dariya ya ce, "To na mara kuma zan goyaki in mun fita, sai kuma me zan yi yanzu ? Kin ga bakiyi murmushi ba."

"Umm umm ni na daina ma murmushi ai kuma?" Gaaji ta fada.

Adnan ya ce, "in dai bakiyi murmushi ba,to ni kuka zanyi ma."

Da sauri tayi murmushi tana, "tom nayi kar ka yi kuka."

, "yawwa Good girl bara in nuna miki wani abu sai mu tafi ko."

Ta ce, "Guduo gu ."

Dariya Adnan ya yi ya ce, "ni fa ba gudou gu bane, Good Boy zakina cewa."

"Tom Gudu bu."

Dariya yayi kawai yana girgiza kai.

Wayarsa ya ciro ya danna video call A WhatsApp likitan da ke kula da baffanta ne ya daga suka gaisa sannan ya bukaci da anuna masa shi.

Nuna wayar ya yi inda Baffan Gaaji yake, yana barci hankalinsa kwance jikinsa har ya fara canjawa.

Tsabar mamaki Gaaji ta kasa magana kusan minti daya kawai ta washe baki tana kallon baffanta nan take Farinciki ya gama bayyana a fuskarta ta ce, "Baffa am Noi ɓanduma? Volwunam,. Anani koiɗum ko?a umman a vawami ko? (Ya jikinka? Ka yi mun magana mana, ka ji sauki ko? Zaka tashi ka goyani?)."
Ta ka baiyi magana ba kallon Adnan ta yi ta ce, "Ka ce ya mun magana ina sho nayi magana da shi."

Adnan ya ce, "ba ki ga barci yake ba? Tunda aka masa aiki bai farka ba sai ya huta sosai inya farka sai mu kara kira ko." Ya karasa maganar yana yiwa likitan Sallama ya katse wayar.

Gaaji cikin yanayin Farinciki ta ce, "Baffana zai ji sauki."

Adnan ya ce, "In Sha Allah yanzu ta shi muje."

Suka shiga Parlourn Uwar Soro suka mata sallama sannan suka fita tare.
A mota ya sata tana ta kalle-kalle da tabe ya koma yawa Yareema magana.

"In ba abun da kake,kadan raka ni wani waje mana?"

"Okay." Kawai Yareema ya amsa.
Ya canja kaya ya fito.

Yana zuwa ya shiga gaban motar, Adnan ya ja su suka dau hanya.

Daga kansa da zaiyi a madubi ya ga Gaaji nata washe baki.
, "Adnan! Kana cikin hankalinka kuwa, Wannan yarinyar fa?"

Adnan ya ce, "Za muje SHOPRITE ne ta sha iska taga abubuwa sannan kuma ina so in mata siyayyan kayan sawa."

"Me zai sa baza ka bada a siyo ba har sai mun fita tare?" Prince Adeel ya fada.

Kafin Adnan ya yi magana karaf Gaaji ta ce, "Ehdin sai anje dani din ina ruwanka ai shi ba dan ishka irinka bane kuma ina shon shi."

Dafe kai Adeel ya yi don takaici yama rasa abun fada.
Adnan ya ce, "zuwa da kanmu da itan ne zaifi wani inya fita da ita za a iya samun matsala."

Daga nan Adeel bai kara cewa komai ba,ban da zafi ba abun da kirjinsa ke yi masa ji yake kamar ya dauki Gaaji ya jefar tsakiyan titi domin ya tsani rashin kunya arayuwarsa,ita kuma ga bakinta kamar barin jinin magana da rashin kunya yake.
Ihbb
Ita kadai da Adnan suke ta surutunsu har suka isa SHOPRITE din.

Tare suka fita duka, suna shiga Suka fara cinkaro da irin Manyan Teddies dinnan da mutane ke shiga ciki.
Ganin abu kamar mutum yana motsi da rawa yasa gaaji ta rikice tuni ta rufe ido tana ihu bata san lokacin da ta kankame Prince Adeel ba.
Saukar wani zazzafan mari kawai taji a fuskarta

Comments,like & Share Fisabillah.

08103080717
[8/9, 12:24 PM] Xayyeesherthul-humaerath🥀:
https://chat.whatsapp.com/C1kXo17nLmb7vCXIubtu5o

*AUREN WATA BAKWAI*

*NOBLE WRITERS ASSOCIATION*

© *Xayyeesherthul-humaerath*

Page-15&16

*Na ce ko zaku ramawa Gaaji marin ne? Na lura kun hasala da yawa😂to meya hwaru ne?🤣*

★★Marin ya shiga jikinta sosai sai da taji canji tun daga kwakwalwar kanta har kafa, wani guntun suma ne ya risketa take hannunta rike da kumatu ban da hawaye ba abun da take kwalalarwa, tuni fuska ta damule da hartsin majina da hawayen  dake artabu,Tsigan jikinta duk ya tashi daga nesa ana iya fahimtar cewa ta shiga wani yanayi da ya firgitar da ita.

Adnan ya ce, "Haba Prince? Wai me yasa kake yiwa yarinyar nan abubuwan da basu kamaceta ba, Don kawai ta rikeka sai ka mareta?"

Prince Adeel Muhammad Rohaan Idanunsa sun fito sosai wanda ya kara bayyanar da bacin ransa karara wanda ana iya jiyo sautin bugawan zuciyarsa.
Kau da kai ya yi ba tare da ya takanwa Adnan ba ya koma mota kawai.
Yana shiga ya dafe kansa yana wani irin huci kaman bijimin Sa.

Adnan ya kalli Gaaji tausayinta ne ratsa masa zuciya a sanyaye ya ce, "Ki yi hakuri kinji ba zai kara marinki ba,bude idonki."
Ya karasa maganar yana miki mata hankicif ta goge fuska.
A hankali ta bude idanun domin  har yanzu taurari basu daina yi mata shawagin zafin marin da taji ba.
Cikin shashshekar kuka ta ce, "Mu gune ,kuma Allah zai saka mun,mai Idon kuliya kawai ni ba ruwana da shi."

Adnan ya ce, "Naji dai yanzu share hancinki muje ciki in siya miki kayan kawai sai mu koma gida ko?"

Ta girgiza masa kai tana share hanci, tana gamawa suka shige cikin SHOPRITE din, tare suke Adnan ne da kanshi ke zaɓa mata kaya, tana bin bayansa da kalle-kalle, Wani Pad ta gani kato ta dauka ta na, "Aboki ka siya mun wannan burodin zaiyi dadi ko? Baba Uwar Soro na bani irinsa ai."

Adnan na karba ya ga Pad ne maimakon Bread din da take fada ya ce, "Aa fa wannan ba Bread bane Gaaji wani abunne daban."

"To mene ne in ba burodi ba? Aradun Allah burodine ai ko lokacin ma da Baffana yana siyomin in ya shigo birni nidai ka siyamun." Ta fada tana taɓe fuska.

Adnan ya karba kawai yasa cikin besket din ba tare da ya ce komai ba.
Kara dauko wasu guda biyu tayi ta ce, "Yo ai Aradu wa inshen sunmun kadan akara wa innan su zama uku yau inta shin abuna in ji dadi."

Shi kam dai bai ce mata komai ba tasa a ciki.
Kaya ya zaɓa mata daidai wa inda zasu mata dogayan riguna da wasu mini hijab, chocolate ,sweet da su biscuit ma kamar wa inda zasu bude provisions ban da washe baki ba abun da take tana jin dadi.

Saida suka gama tas kafin suka koma mota, Prince na ciki yana danna waya, sai da Adnan ya budewa Gaaji ta shiga sannan shima ya shiga, tana shiga tayi tsaki da kwafa, ganin Adeel bai ma san tana yi ba ta dunga dage tana harararsa da murguda masa baki.
Kamar ance ya kalli morrown gaban motan suka hada ta takarkare tana murguda masa karamin bakinta ta ko ina a fuskarta ba inda baya motsi.

Kawar da kansa ya yi kamar bai ganta ba don ya fara fahimtar Indai ya biyewa wannan yarinyar sai ta maidasa karamin mahaukaci.
Kan su isa Fada an fara kiran sallan magriba, haka yasa Adnan ya na aje mota ya bude mata cikin sauri ya ce tazo ya maida ta ciki gun Uwar Soro tun kafin wani ya gansu.
Ita kuwa Gaaji tsayawa tayi lallai fa sai ta ci gaba da murgudawa Adeel baki kan ya fito a motar taje tana kokarin tura kanta daidai da lokacin da yake kokarin turo kofar ya fito bai na ganta ba.
Da sauri Adnan yaja hannunta yana, "kina so muyi fada ko? Baki ga lokacin sallah ya yi bane? Oya muje ki shiga ciki muma zamu shiga Masallaci."

Shigewa tayi da tarin ledar kayanta guda biyu tana juyowa tana daga masa hannu a dole byeebyee.

Aiko tana shiga ciki ta baza kayan nan kaf a kasa tana murna take ta cire kayan fulaninta tasa wata Abaya ta mata kyau Sosai, Uwar Soro kuwa binta da kallo take kawai na mamaki ganin yau da kanta ta cire kayan Gadonta tasa wani ah lallai Gaaji an fara canjawa.

Ita kadai tana ta sambatu, "Ai aradu ba a tabani a zauna lafiya She na gyarawa mutum hankali tunda shi an ishka ne kuma mugu, Shi kam Abokina ba ruwansa Dan albarka she siyamun kaya yake."
Pad dinnan ta ciro ta jera gabanta tana, "Yawwa wannan Burodin zanci yau Baba ba zan ci abinshinki ba abokina ne ya sayo mun mai dadi."

Uwar Soro ta ce, "Mu ga Burodin naki Gaaji."

Tashi tayi tana yage ledar ta ce, "Kadan fa zan sammaki ba duka ba ,zan shi abina duka ni kadai."

Uwar Soro na karba ta ce, "Wannan ai Audugace ba burodi ba."

Gaaji ta karbe abunta tana, "Audugar me? Burodi ne fa aboki ya siyamun."

Dariya Uwar Soro ta yi ta ce, "na san dai kin fara al'ada to Da kika fara jini na fito miki da me kike amfani lokacin kina Ruga?"

Gaaji ta ce, "Ni tsumma nake sawa in tare sai ranar da naga jinin ya dauke sai in Jefar a shara."

Da sauri Uwar Soro ta riketa ta ce, "Subhanallahi to wannan abun ake sawa ba tsumma ba,kin san tsumma kuwa cuta yake sawa? Zai saki ki yi tsutsa,yana fito miki kuma kina wari a karshe ma ki mutu."
Nan take Gaaji ta gwalalo ido tsoro ya gama cikata.
Uwar Soro ta ci gaba da cewa, "Kin ga shi wannan kullum ma in kina yi a kalla sau biyu ko sau uku ake so kina canja wani,da zaran ya baci ko ya dan dau lokaci ake cirewa saboda gujewa

shigar wata cuta kinji ko?"

Jikinta ya yi sanyi ta ce, "ni kam ba zan kara sa tsumma ba kar inyi tsutsa Ysn ba ruwana na daina, tun yanzu ma zansa wannan din ya fara taremun kafin ya zo."

Uwar Soro ta yi Murmushi tana, "Aa ai sai yazo ake sawa yanzu zan boye miki kinji baza ki yi tsutsa ba In Sha Allah."

Saida Adnan ya dawo ya mata tatsuniya kafin tayi barci kuma ya tafi.

★★
Khalesa ban da zabga kira a waya ba abun da take yiwa Adeel ya ki dauka da ta gaji kawai sai ta nufi bangarensa tana zuwa ta tatarar da shi tsaye da Nasmah suna magana.

Wani irin kallon raini ta bi Nasmah da shi, ita ma ta maida mata da kallon tara saura kwata. Karasa tayi daf da Adeel ta ce, "Prince na zo gunka ne fa kuma na ga wata."

Adeel ya ce, "Nasmah ce ai dukan ku ɗayane."

Cikin bacin rai Khalesa ta ce, "Aa wallahi ni da ita ba ɗaya bane kama daina haɗamu ko a shekaru na fita bare kuma batun kasancewa gareka muna da tazarana matsayina daban nata daban, so ta bani waje ina so inyi magana da kai."

Nasmah tayi murmushi kawai tana kallonta.

Prince Adeel ya yi shiru shima ba tare da ya ce komai ba sun maidata fanko kawai.

A har zuke ta kara fadin, "Magana fa nake, ke Nasmah wai ba kyajine? matar sa na son yin magana da shi?"

"Matata?" Yareema ya fada cike da mamaki fal a fuskarsa.

"Eheen ko ka manta ne?"
Khalesa ta fada cikin isa.

Ya ce, "ke da ita duk dayane duk abun da zaki fada ki fada gabanta zai fi miki."

Wani irin fusata Khalesa tayi tana sakin tsaki ta kara bin Nasmah da wani kallo tare da yin kwafa,ita kuwa Nasmah gwalo ta mata da wata irin dariyar mugunta.

Nasmah na ganin Khalesa ta tafi murya a raunane ta ce, "Na dameka ko Prince? Sorry Gudnyt ka je ka kwanta ka huta gobe kawai mayi maganar ko Lokacin da kake free ka kula da kanka."

"Alright thanks." Ya fada kawai ya shige.

Sai da taga shigewarsa sannan ta tafi tana sakin murmishin da ita kadai ta san Dalilin sa.

★★★Misalin karfe Tara na safe Gaaji ta sha wanka ta karasa kaya da ɗaya cikin wanda Adnan ya siya mata sau juyi ake, ranar ba fada ta tsaya aka mata wanka tayi brush da kanta, wanke dambun gashin ta ne dai har yanzu taki Yarda Uwar Soro ta taba bare a wanke mata shi.

Daukan hanya tayi bijigun-bijigun zata fita, Uwar Soro ta ce, "Ina zuwa?"
Tunani ta tsaya yi ta tana sakawa a zuciyar ta indai ta fadawa Uwar Soro asalin abun da zata yi bazata barta ba , can sai ta washe baki ta ce, "Zan ni in nunawa abokina Adona ne ns irin kayan yan birnin da ya shiyamun inshe mishi na gode."

Uwar Soro ta ce, "to kardai kiyi wani gun kina fita ki shiga can in ba haka ba ana kamaki yanki ki za ayi na fada miki."

Gaaji ta ce to sannan ta fice.
Bin bayanta Uwar Soro tayi saida ta tabbatar ta shiga bangaren Yareema kafin ta dawo nata bangaren.

A hankali ta tura kofar ta shige.
Tana shiga kuwa taga Yareema na barci hankalinsa kwance daga shi sai gajeran wando.

Ta ce, "Ji an ishka barcinma ba kaya yake yi aiki yau zaka shi gidanku aradu."
Ta karasa gabansa a hankali tana zuwa ta sake masa mari a kumatu tauuu ta kara sake wani tauuu.
Yareema ji ya yi kamar a maraki ana zabga masa wasu irin zafafan maruka.
Ya yi saurin bude idonsa ya ganta tsaye kansa amman ya kasa gasgata hakan.
Rike hannu tayi a kugu tana fadin, "Kalle ni da kyau mai idon mage nishe nan Zainabu Gaajin Baffa ramawa na zo yi na rama marin da kamun ehee kai ma Kaji inda Dadi ai da wani wandon ka kamar nafkin."

Sai a lokacin ya tabbatar da a zahiri yake kokarin tashi ya fara a fusace.
Ai Gaaji da taja dogayen kafafunta masu kama da sandar sunuka sai waje.

Tashi ya yi ya.........

*TO FA FREE PAGES NA DAF DA KAREWA SAURA PAGES BIYU IN SHA ALLAH, ZAKU IYA FARA PAYMENT YANZU ₦300 KACAL VIA 1453215759 Aisha Abdullahi Sani Access Bank

Evidence of payment to 08103080717*

Luvs U Oll😘🫶💃😻
[8/9, 8:47 PM] Xayyeesherthul-humaerath🥀: *AUREN WATA BAKWAI*

*NOBLE WRITERS ASSOCIATION*

© *Xayyeesherthul-humaerath*

Page-17&18

Cikin Fushi zai fita har sai da yaje bakin kofa ya tuna da gajeran wando ne a jikinsa, tsaki ya yi ya koma,yana zura jallabiya ya fita zuwa bangaren Uwar Soro.

Gaaji na ganin shigarsa da gudu ta koma bayan Uwar Soro tana kankameta, "Baba Wallahi shin zalina zai kara yi don kawai na rama marin da ya mun."

Bude baki Uwar Soro tayi da mamaki tana kallon Gaaji ,Don ita a iya saninta babu wani mahalukin da ya taba dagawa Yareema hannu,bare kuma batun mari, ah lallai Yar nan kin taro ruwa.
Ta fada aranta.

Yanayin yadda yake huci ita kanta Uwar Soro ta razana ta yadda ta kasa ce masa uffan.
Gaaji kuwa kara kankameta take tana, "Aradu mugune karki bari ya taɓani zai kashe ni."
Ji tayi kawai ya dauketa cak.
Ya fice da ita,ba direta a ko ina ba sai kofar wani kurkukun daki, karami, mai bala'in duhu mutum baya iya ganin ko hannunsa a ciki, jefata ciki ya yi ya rufe kofar sannan ya koma dakinsa.

Nan take Gaaji ta birkice, Wani irin kuka take tamkar ba mutum ba, ta gama ficewa a hayyacinta, kayanta duk ta yayyaga su da fisga,gashin kanta ma sunyi carko-carko, tana ta fisga cikin lokaci kalilan ta dawo mahaukaciya.

Uwar Soro kuwa Tana ganin Prince Adeel ya shigar da Gaaji dakin nan hankalinta ya matukar tashi,tasan Manya ma aka shigar da su ya suka kare bare kuma mutum? Dakin da babu ko windo bare wani sakon da haske zai shiga, nunfashi ma mutum na ciki in ya dau lokaci dakyar yake iya yi, wasu ma kan a cirosu sun mutu.

Ganin bata da wata mafita yasata saurin kiran Adnan ta sanar da shi halin da ake ciki, Wayar Adnan sam bata shiga domin ya tafi India gun aikin Baban Gaaji Ya duba yadda lamuran ke gudana, kuma daga nan zai koma America domin yin wani bincike da yake.

Tun tana gwada kiran har ta gaji ta hakura, domin babu alamar shiga.

Adnan ya sanar da shamaki cewa bai yarda wani yaje Gaaji take ba sai shi,kuma shi ma din ruwa kadai zaina bata kada a kuskura a bata abinci.

Gaaji tun tana ihu har ta gaji ta daina ban da ajiyar zuciya babu abun da take,kamar wasa har dare ya yi,ya tabbata dai sai da ta kwana adakin, duk da cewa ita batasan dare ko rana ba saidai wani lokacin kawai ta ji barci ya dauketa, inko ta farka ma duk daya tunda duk abu ɗaya idonta ke gani wato duhu,barcinma tana farawa wasu irin samudawan sauro zasu isheta da kuka a kunne, a jiki suna cizo, ya zamana bata da aikin yin da ya zarce kuka.

Uwar Soro ce ta roki shamaki da ya taimaka yana bata abinci ko da kadan ne ba tare da sanin Yareema ba, tunda ita ma ya ce ba ruwanta kada ta bari a hannunta ya shiga ciki,hakan kuwa ya kasance a boye kullum yake bata abinci da ruwa.
Gaaji na cin abinci tana kuka,laluba take domin ko bakinta ma takan iya rasawa wani abincin ma kan ya shiga bakinta ta zubar a lalube lalube,kusan rabin abincin a kasa yake,kafin rabi ya shiga cikinta.

Ranar da ta kwana uku a dakin Adnan ya dawo,yana zuwa MASARAUTAR bangaren Uwar Soro ya fara nufa domin ya yiwa Gaaji tsaraba sosai kasancewar yasan zai sha daru zata ce yaki zuwa gunta inko yace yayi tafiyane ma zata ce me yasa bai tafi da ita ba.

Da fara'arsa ya shiga yana fadin, "Wai ina Gaaji Beautyn ne? Tana ina? Bata ji Yayanta ya zo bane? Ko dai fushi tayi ne? In fara tsallen kwado daga nesa ko? To na fara."
Ya ƙarasa maganar yana shiga cikin Parlourn Uwar soro, tsayawa ya yi turus ganin Uwar Soro ce ita kadai babu Gaaji bare alamar ta.

Ya ce, "Kardai fushin yasa ta buya bata son ganina?"

Cikin yanayi na rashin jin dadi Uwar Soro ta ce, "Ina fa, Gaaji na dakin Duhu."

Zaro ido Adnan ya yi cikin fargaba ya ce, "Subhanallahi! Me ya faru? Waya kaita?"

Nan da nan Uwar Soro ta kwashe dukkanin abun da ya faru ta sanar da Adnan.

Ko magana bai kara ba cikin fushi ya nufi gun Adeel.
Yana shiga Yaga Adeel hankali kwance yana zaune a daining yana cin abinci.
Ko sallama gagararsa ta yi yana shiga kawai a harzuke ya ce, "Akan me zaka Rufe Gaaji a wancen dakin duhun? Nikam wai ina imaninka ne Prince? Me yasa zaka kulleta kullewan ma bana lokaci kadan ba yau har kwana uku? Wannan Yarinyar Amana ce fa agunka Wallahi in har ka cutar da ita wani abu ya sameta Ubangiji ba zai taba barinka,me yasa zaka aikata haka?"

A gajarce Adeel ya ce, "saboda na isa na yi mata hukunci a matsayina na mijinta."

Kallonsa Adnan ya tsaya yi da mamaki,wai har Adeel ne ke dangata kansa da Gaaji matsayin miji,abun da bai taba furtawa ba koda da wasa?
Ya ce, "To naji ni kuma a matsayina wanda nake yaya awajenta ka fitomun da kanwata."

Adeel ya tashi ya nufi 2sita ya zauna kafin ya ce, "Baka isa ba,in kuma kace zaka shiga sabgar da ba taka ba zan nuna maka asalin wane ne Prince Adeel Muhammad Rohaan."

Ran Adnan ya matukar kara ɓaci zuciyarsa na bugawa cikin zafin rai ya ce, "Au haka za ayi? Ya karasa maganar ya bugawa Adeel hannu a kirji.

Adeel ma a fusace ya buga masa kirji yana fadin , "Kwarai."
Kokarin fara kokuwa suka yi kowannensu na wuce zuciyar maza na bugu rai ya baci.
Uwar Soro ce ta katse su da fadin, "Subhanallahi! Me zan gani? Me yake shirin faruwa anan kuma,da girmanku?"

Adnan na wuce ya ce, "Na rantse da girman Allah indai yau bai fito da Yarinyar nan ba babu shakka sai na je Fada na sanar da Mai Martaba da kowa ma , in tabbatar da cewa gata nan matarsa ce."

Cikin fushi ADEEL ya wurga masa keyn dakin yana huci ya shige cikin bed room.
Adnan ya fice Uwar Soro ma ta bi bayansa suna zuwa cikin sauri jikinsa na rawa ya bude Gaaji.
Hasken da tagani ya kashe mata ido rufe idon tayi a tsorace ,haske har ya fara zame mata sabon abu.

Uwar Soro ce ta shige ta riko hannunta da sauri ta fito da ita.
Gabadaya yanayinta ya canja mata da maraba da mahaukaciya har ta fi fasali lokacin da ta fara zuwa fadan akan yanzu.
Jikinta duk wasu irin cuhuka da kuraje.
Idonta arufe ban da hawaye babu abun da take.
Adnan ya tsaya yana kallonta bai san lokacin da hawaye suka fara zuba daga idanunsa ba jikinsa kuwa ya kasa daina rawa.

Cikin Muryar kuka ta ce, "Ina za akaini? Don Allah kar amaidani irin wancen dakin zan mutu."

Uwar Soro ta ce, "ba za amaidaki ba, Gimbiyata nice nan kinji daga yau ma baza ki kara shiga cikin dakin ba In Sha Allah,ki bude idon ki a hankali kinji mu tafi."

Tana bude ido tana ganin haske sai ta kara rufewa a karshe sai haka suka tafi kawai.
Adnan kumq tsabar tausayinta ya kasa furta komai ma sai binsu da kallo kawai.

Suna shigewa cikin daki shima ya fice a Masarautar rai bace ba tare da ya koma bangaren Prince ba.

Dakyar ta iya bude ido , uwar Soro ta mata wanka ,ana wankanma tana kuka domin ko ina aka taba ciwo yake mata,dakyar aka wanke mata jikin sama-sama ta sha magani, duk son abincin Gaaji kasa ci tayi dakyar tasha tea dan kadan ta kwanta barci.

Tana barcinma ban da razana ,ihu da surutai babu abun da take tana birgita, sai da Uwar Soro ta mata addu'a  to tofa mata sannan ta samu barcin nata ya danyi nisa.

Gabadaya duk ta kumbura,har yanayin kamanninta ya canja.

Tun daga Ranar Adnan ko ya shiga fada baya neman Adeel sai dai ya duba Gaaji suyi hira ya tafi, ko da sun hadu da Yareema sai dai kowa ya yi harkar gabansa ba mai kula Wani.

Ita kuwa Gaaji na zaune sai dai aji tayi kwafa, in Adeel ko Uwar Soro suka ce mene ne? Saidai kawai ta washe baki ta ce ba komai.

Daukan Gaaji Adnan ya yi zasu fita kenan sai ga Adeel ma ya fito suka ci karo da juna Gaaji ta.....

*Second to the last free page, ka da a manta gobe za a gaba free pages in sha Allah , duk mai son ci gaba da karantawa zata biya ₦300 kacal via 1453215759 Aisha Abdullahi Sani Access Bank, masu Opay kuma 8103080717, Evidence of payment to 08103080717, can't' luv you less oll😘😘😘😘*

Urs Xayyeesherthuo
[8/11, 8:42 PM] Xayyeesherthul-humaerath🥀: *AUREN WATA BAKWAI*

*NOBLE WRITERS ASSOCIATION*

© *Xayyeesherthul-humaerath*

Page-19&20

*Last Free Page*

Kallon juna suka yi na tsayin daƙiƙo, Everyone has the thoughts that are in his heart, A hankali cike da nutsuwa Prince ya yake kallon hannunsu da yake sarƙafe dana juna, gently kuma ya zame idanunsa without knowing yadda ya fahimci abun, ya nemi waje can saman ladduma mai taushi da wani kumbo a gefe ya zauna, ya gyara zama farar Alkyabbar dake jininsa, yau ya tuna da cewa shi ɗin jinin sarauta ne.

"Hold on.." ya furta shortly yana ɗauke kai tare da mai da ganinsa kan wayar da yake dannawa, Adnan ya tsaya sai kuma ya juya yana cewa "Is there any problem?" Prince ya yatsuna fuska ya ce "No!" Ya sauke numfashi, sai kuma ya ɗago kai bakiɗaya yana zubawa Adnan idanu sai kuma ya mayar kan Fulani gul ɗin calmly ya ce "Baka jin kunyar fita da wannan datti gal ɗin? Why you're always making problem? Baka jin kunyar jama'ar masarauta?"

"Masarauta? The royal kingdom, or kuyangi, ko barori, hadimai? Jakadan fada ko hakimai? Dagatai ko masu unguwarmu? Ko mutanen da kake mulki, wanne kake so na ji kunya danna fita da Zainab?" Ya yi murmushi yana neman wajan zama looking at yarima's direction ya ce "Tell me something Prince Adeel, do you love her?" Cikin sanyin murya Adeel ya ce

"Goodness, love? Me da wancan? Ka ke imagine ko a reflection kaga haka? Har gaban abada babu wannan" Ya faɗa so Clam Adnan ya ce "Ohk, am so happy for that, idan haka ne mu yi deal mana"
"For?" Prince asked. Adnan ya ce "Baka san Zainab Gaaji, kuma AUREN WATA BAKWAI ne, da lokaci ya yi zaka bata divorce paper, idan ka saketa ni zan aureta, amincewarka nake nema wanda kuma shi ne zai tabbatar mini da cewa baka son ta, idan na aureta zama mu iya bar maka country ɗin bakiɗaya bama masarauta ba Ohk"

Tunda ya fara magana kan Prince yake a ƙasa bai ɗago ba, balle a fahimci yanayinsa, ya riƙe kansa da kyau. "All ears, deal?" A hankali ya ɗago kai ya ce "Deal, na amince ka aureta i don't have any problem with that" Gaaji ya mike ta shiga tsalle tana rawa ta ce "Aradun Allah na ji daɗi, mugu zai sakeni kai ka aureni shaaii Gaaji ƴar gata jiki mai laushi ga kamar buduri kullum kana mini doki, shaai dai kada ka dinga zama tsirara ana ganin wannan jelar na lilo irin ta Wannan mugun wata zalmaƙeƙiyya" Adnan ya runtse idanunsa trying to Calm himself down kana ya zaro paper da pen ya bawa Prince ya ce "Sign... I am coming"

Adnan na fita not too long ya dawo tare da Uwar soro, ya labarta mata komai don ta zama shaida, ta juya ta kalli Prince sosai ta ce

"Kuma da gaske baka son ta? Sakinta za ka yi?" Ya jinjina kai alamar eh ta ce "Ka bani mamaki bayin zaton haka ba" Silently ya ce "To me kika zata?"

"Zaka zauna da ita, zama na har abada zata zama Fulanin masarautar nan watarana domin na gano hasken hakan a tare ita" Ya yi shiru kawai kansa a ƙasa ta ce

"Ba damuwa, hakan ba laifi bane, zaka dawo watarana ina zaune a nan zaka sha mamaki a lokacin, Adnan zan tsaya maka ka auri Gaaji da zarar wata bakwai ya yi" Ta juya kan Prince ta ce "And you, kada ka sake ko da wasa ka ce zaka ɗora mata idda balle ka lalata mata rayuwa a iska, Adnan Sannunku Ubangiji ya biyaka tabbas ka yi sacrifice zaka samu farin ciki" Prince ya yi sign ya fice har ya je bakin ƙofa ya ce

"As frm today ba ruwansa da ita, ya jira sanda zamu rabu" Yana faɗin hakan ya fice bai basu wani opportunity na yi masa magana ba, Adnan ya kalli Gaaji dake Kallonsa without blinking her eyes "I I..." Sai kuma ya fasa faɗa and he just quickly leave the room.

A week after the Adnan and Prince deal.. Gaaji na zaune ta ɗan fara sauya ta koma shiru shiru sbd rashin ganin Bestie ɗinta Adnan, duk da cewa ba komai ta fahimta amma tasan faɗa sukai sosai da mugun mutumin can sai tsanar shi ta ninku a ranta fiye da kima. Kamar daga sama ta ji an ɗaga labule an shigo kallon kallon sukai da ita da Jakadiyya, Jakadiyya ta kalli Gaaji tana son fahimtar wace gani tayi kamar tana mata gwalo ta murza idanu ta rufe tana buɗewa taga babu komai a wajan, sai empty space ana haka Uwar Soro ta fito ta ce "A'a Jakadiyya ce?" Jakadiyya ta ce "Wallahi nace bari na leƙo mu gaisa uwar ɗakin Yarima" Murmushi kawai Uwar soro tayi sai kuma Jakadiyya ta ce "Ranki ya daɗe Uwar soro meke faruwa ne?" Ta ce "Dame?" Ta ce "Baƙuwa na gani a nan kamar Bafullatana" Da shocke ta ce "Stranger? A nan? Kai sai idan Aljanu suka buɗe miki idanu musamman ma kin ce kamar Bafullatana, kin san haka nan Aljanu suke da buɗe ido balle masarautar mai siddabaru da tsibbu iri-iri kowa ya zama ruɓaɓɓe" Cikin Jakadiyya ya kaɗa musamman data tuna gwalon da Gaaji tayi mata, ai da sauri ta fice sbd gudawar daya zo mata kenan aljanna ta gani yau ta shiga uku.

Tana fita Gaaji ta fito idanunta jajur jikinta sai rawa yake kanta a ƙasa tunda sukai idanu biyu da Jakadiyya yanayinta ya sauya gabaɗaya.
Ganin ta fito jikinta a sanyaye Uwar Soro ta ce,"Mene ne ya faru Gaaji?"

Shiru tayi sai da ta kwanta a jikinta kafin ta ce, "Kaina ciwo,kaina ciwo ike mun,bana son ganin waccer muguwar bana sonta."
Wasu irin sambatu ta fara, Uwar Soro ta riketa saida ta tofa mata addu'o'i kafin ta dawo daidai.

Ita ma Jakadiya tafiya tayi jikinta a sanyaye gabaɗaya ta gama tsorata aranta tana tuna cewa ance fa duk ranar da Mutum ya yi ido biyu da Aljanu to mutuwa zaiyi, idonta yayi luɓu-luɓu ta fito a sak asalin ƙasungumar munafuka, tintibe tayi bata sani ba zata fadi ta saki wata irin kara tana , "Na shiga uku, Kwana na bai kare ba da saura Don girman Allah ku rufa mun asiri." Ta fada tana rufe ido.

Ranar kasa samun sukuni tayi bare a samu damar nemo rahoto,dakinta ma ta gagara shiga gani take tana shiga zata mutu,abu kadan kuwa zata razana tana fadin, "Na shiga uku Ba mutuwa na zo yi ba." In akace me ya faru sai ta fara inda-inda.

★★★★

Misalin 8 na dare Gaaji ta saci hanya ta nufi part ɗin Prince a tunaninta ko za taga Adnan a ciki, a hankali take shiga har ta shige parlour babu motsin kowa ta nufi bedroom, zaune ta gansa saman carpet ya tankwashe ƙafarsa ga plate ɗin abinci a gabansa da kuma wata babbar warmer, daga shi sai gajeren wando da armless, tunda ta shigo idanunta ya sauka akan abincin jikinta ya ɗauki rawa idanunta sukai wani masifaffan jaa yana ƙoƙarin kai spoon bakinsa ta kwarara wani uban ihu tayi kansa suka faɗa saman carpet wani ƙanƙame shi tayi tana ihu da gurnani tana dukan ƙirjinsa yanayin ihun da take bai kama dana mutum ba, ganin hakan yasa Prince buɗe hannayensa ya shigar da ita faffaɗan ƙirjinsa ya rungumeta tsam yana shafa kanta a hankali ya ce "Heee Zizi, what happens?" Ihu take tana sandarewa ya miƙe da ita tsam a jikinsa ya nufi other room ɗinsa, daman tun safe yake jin wata masifaffiyar sha'awa kamar zai mutu yanzu daya jita a jikinsa ta ƙara hura masa wutar abinda yake ji, a ransa yana jin wannan opportunity ne ya samu da zai rabata da budurcinta tunda bata hayyacinta, ai ya biya sadaki ya cinyeta tas ya amshe budurcinta ya rubuta takardar sakin yabar ƙasar bakiɗaya idan ya so, Adnan ya auri empty raguwar shi, da wannan tunani ya cillata saman gado yana kashe switch ɗin bedroom ɗin ya zame kayansa yana jin kamar mararsa tayi tsalle ta tsinke daga jikinsa sbd yadda take fisga cikin goshewar hankali ya faɗa saman gadon tare da fizgota ya.....

*Free Pages sun kare duk wacce take son ci gaba da karantawa zata biya 300 kacal via 1453215759 Aisha Abdullahi Sani Access Bank, Opay users 8103080717 Aisha Abdullahi Sani, evidence of payment to 08103080717 Luv U Oll🥰🥰😘😘♥♥*

Urs Xayyeesherthuo